من هم أحباب أهل البيت؟

بلغة الهوسا

تأليف محمد المنصور إبراهيم

# SU WANE NE
# MASOYAN
# AHLUL BAITI ?

WALLAFAR :

MUHAMMAD MANSUR IBRAHIM

SOKOTO

**FASSARAR:**

ALIYU RUFA’I GUSAU

Bugawa da Yaɗawa:

**Mu'assatu Ahlilbaiti Wassahabah,**

**Nigeria**

(C) 2005

ABUBAWAN DA KE CIKI

**Godiya**
**Sadaukarwa**
**Gabatarwar Mai fassara**
**Gabatarwar Mawallafi**

BABI NA ƊAYA
1.0 Iyalan Gidan Manzon Allah (SAW)
1.1 Ma'anar Iyalan Gida
1.2 Dangogin Manzon Allah (SAW):
1.3 Babannin Manzon Allah (SAW) da Gwaggonninsa ('Yan uwan Haihuwar Mahaifinsa)
1.4 Yanne da Kannen Manzon Allah (SAW) maza da mata ('ya'yan 'Yan uwan Mahaifinsa.
1.5 Kawunnen Manzon Allah (SAW) da Innoninsa ('Yan uwan Haihuwar Mahaifiyarsa maza da mata
1.6 Matan Manzon Allah (RA)
1.7 'Ya'yan Manzon Allah (SAW) Maza da Mata

BABI NA BIYU

2,0 Martabobin Ahlulbaiti
2.1 A cikin Al-ƙur'ani
2.2 A cikin Hadisi (Sunna)
2.3 Haƙƙoƙin Ahlulbaiti akan Musulmi

BABI NA UKU
3.0 Alaƙar Magabata da Ahlulbaiti
3.1 Matsayin Ahlulbaiti a wurin Magabata
3.2 Auratayya Tsakanin Ahlulbaiti da Sahabbai da Tabi'ai

BABI NA HUƊU
4.0 Ahlulbaiti a wurin Rafilawa
4.1 Su wane ne Ahlulbaiti a wurinsu?
4.2 Sun raba ɗaya Biyu

BABI NA BIYAR
5.0 Matsayin Ahlulbaiti game da Rafilawa ('yan Shi'ah)
5.1 Matsayin Ali Ɗan Abu Ɗalib (RA)
5.2 Matsayin Hassan Ɗan Ali (RA)
5.3 Matsayin Hussaini Ɗan Ali (RA)

5.4 Matsayin sauran Ahlulbaiti

5.5 Bukukuwan Ashura
5.6 Naɗewa.

# GABATARWAR MAI FASSARA

Yahudawa da Nasara, maƙiya addinin Musulunci, sun yi ƙoƙarin saƙa tunanin 'yan Shi'ah, da gwada mu su cewa addinin musulunci addini ne na 'yan gidanci. Saboda haka sai suka taƙaita shugabancin al'umma – wanda aka san shi a matsayin Shawara tsakanin musulmi – su ka mai da shi haƙƙi ga iyalan gidan Manzon Allah **"Ahlulbaiti".** To da ma abin ya tsaya nan, da sauƙi. Sai kuma daga cikin iyalin na Manzon Allah (SAW), suka ware wasu, suka ce ba da su ba a ciki. Abin kuma bai tsaya ga wariyar ba, sai kuma suka bi su da, bi-ta-da-ƙullin sukar lamiri da tozartawa, su na jifarsu da ƙazafi da miyagun lafuzza.

A cikin ɗan wannan littafi, Malam Muhammad Mansur Ibrahim Sakkwato, ya yi ƙoƙarin feɗe wa mai karatu biri har wutsiya, game da waɗanda ke iya shiga ƙarƙashin tutar iyalan gidan Manzon (SAW). Ya kuma bayyana irin darajoji da suka keɓanta da su. Sa'annan ya ba da haske game da matsayin Ahlul Sunnah da na 'yan Shi'ah akansu ta yadda, mai karatu zai iya

yanke hukunci da kansa "Su wane ne **Masoyan Ahlulbaiti**"?

Malam Mansur ya yi amfani da ayoyin Al-ƙur'ani mai girma da Hadissai ingantattu da tatattun bayanai na tarihi, don gamsar da mai karatu da ingancin hujjarsa. Ya kuma yi adalcin mayar da ko wace magana zuwa ga mai ita daga marubutan Sunnah da na Shi'ah baki ɗaya. Wannan littafi zai taimaka matuƙa wajen gane bakin zaren abinda ya shafi **Ahlulbaiti** da masoyansu, musamman ga matasa masu kishin musulunci.

Na samu wannan ɗan littafi nasa rubuce ne da larabci duk da yake ya gabatar da shi da Hausa a matsayin Lacca a wurare daban daban. A zatona samun wannan littafi da Hausa a wannan ƙasa tamu yafi alfanu bisa ga kasancewarshi da larabci. Don haka na yi gaggawar yin wannan aiki na fassara shi zuwa harshenmu na Hausa. Da fatar Allah ya ba ni ladar da ke ciki, ya sa kuma mu cimma manufar da mu ka dosa.

Allah Ya yi mana jagora, Amin.

Aliyu Rufa'i Gusau
Sashen Tsare-Tsare, Bincike da Kididdiga.
Ma'aikatar Lamurran Addini ta Jihar Zamfara.

بسم الله الرحمن الرحيم

## Gabatarwar Mawallafi

Bayyanar aƙidar Shi'a a Najeriya ta arewa ya zo ne bayan juyin juya halin da aka yi a Iran a ƙarƙashin jagorancin Ayatullahi Khumaini a shekarar 1979. Kafin wannan lokaci dukkan musulmi a wannan yanki, su na bisa ga turbar Sunnah ce wadda Mujaddadi Usmanu ɗan Fodiyo (Allah ya ƙara ma sa rahama) ya sabunta.

A bisa ga wannan turba, dukkan musulmin wannan ƙasa su na mutunta iyalan gidan Manzon Allah (SAW) tare da Sahabbansa. Alal Misali, ba za ka iya ƙirge masu sunan Fatima ba, haka ma Hassan da Hussaini a gidajen Musulmi a wannan ƙasa. Haka nan masu ɗauke da sunayen matayen Manzon Allah (SAW) kamar su Khadijah da A'ishah da Hafsah, haka ma sauran 'ya'yansa, kamar Su Zainab da Ruƙayyah. Haka kuma lamarin ya ke game da Sahabban Manzon Allah (SAW), tun ma ba Halifofin da su ka biyo bayansa ba, wato,

Abubakar da Umar da Usmanu da Aliyu, da kuma sauran Sahabbai.

Aƙidar Shi'a ita kuma ta ginu ne akan wariya a tsakanin waɗannan tsarkakakkun bayin Allah waɗanda su ka samu tarbiyyarsu daga hannun Manzon Allah (SAW), a daidai lokacin da alƙur'ani ya ke saukowa da ɗiminsa. 'Yan Shi'ah sun rungumi iyalan gidan Manzon Allah ne kawai, su ka bar almajiransa. Kuma sun kitsa wasu irin tatsuniyoyi marasa tushe don su labarta cewa, wai akwai adawa da gaba a tsakaninsu.

Wannan bincike ya zo ne don feɗe gaskiya game da lamarin, ya kuma soma da wannan tambaya, ita ce: "Su wane ne Masoyan **Ahlulbaiti**"? Don samar da amsarta kuwa, sai binciken ya fantsama a cikin maɓuɓɓugar aƙidun Sunnah da na Shi'ah a game da **Ahlulbaiti** ta yadda mai karatu da kansa daga ƙarshe zai bai wa kansa amsar wannan tambaya.

Malam Aliyu Rufa'i ya yi amfani da takardun binciken da kuma kaset kaset ɗin laccocin da aka gabatar da wannan binciken a wurare daban daban na jihohin Arewacin

Najeriya. Don haka, aikin nasa ya fito mafi kusa da sigar da mai binciken zai iya fitowa da ita da shi ne ya fassara. Amma duk da haka, na sake nazarin aikin baki ɗaya, tare da komawa ga wasu daga cikin manazartar binciken don ƙara tantance sahihancinsu.

Ina roƙon Allah ya saka ma sa da alherinsa, ya sa aikin ya zamo jagoran shiriya ga masu neman gaskiya.

Baban Ramlatu,

Muhammad Mansur Ibrahim

A Birnin Iskandariyyah, ta ƙasar Misra

Daren 14 ga Shawwal 1426B.H/ 15 ga Nuwamba 2005M

# BABI NA ƊAYA
## 1.0 Iyalan Gidan Manzon Allah

Wannan babi zai yi bayani ne, a kan abinda kalmar 'Iyali' ke nufi, tare kuma da biyar daddagin jinsin mutanen da, ke iya shiga ƙarƙashin tutar Iyalan gidan Manzon Allah (SAW) na daga danginsa, na wajen uwa da uba, matansa, 'ya'yansa da zuri'arsa.

### 1.1 Ma'anar Iyalan Gida

Asali, kalmar iyali, a harshen Musulunci na nufin "matar mutum". Iyalin mutum, na nufin matarsa. Kamar yadda Al-ƙur'ani mai tsarki da Sunnar Manzo Allah, suka nuna. Allah (SWT) na cewa akan Matar Annabi Musa (AS):

﴿ فَلَمَّا قَضَى مُوسَى الْأَجَلَ وَسَارَ **بِأَهْلِهِ** آنَسَ مِنْ جَانِبِ الطُّورِ نَارًا قَالَ **لِأَهْلِهِ** امْكُثُوا إِنِّي آنَسْتُ نَارًا لَعَلِّي آتِيكُمْ مِنْهَا بِخَبَرٍ أَوْ جَذْوَةٍ مِنَ النَّارِ لَعَلَّكُمْ تَصْطَلُونَ (٢٩)﴾ [سورة القصص]

Ma’ana:

To, a lokacin da Musa ya ƙare adadin, kuma yana tafiya da Iyalinsa (Matarsa), sai ya tsinkayi wata wuta daga gefen dutse (Ɗuri Sina’a). Ya ce wa Iyalansa (Matarsa),

“ku dakanta, lalle ne ni, na tsinkayi wata wuta, tsa- mmanina ni, mai zo muku ne daga gare ta da wani labari, ko kuwa da guntun makamashi daga wutar don ko kuji ɗumi”

[Suratul Kasas : 29]

Ya kuma ce a kan Annabi Ibrahim (AS) :

﴿هَلْ أَتَاكَ حَدِيثُ ضَيْفِ إِبْرَاهِيمَ الْمُكْرَمِينَ
(٢٤) إِذْ دَخَلُوا عَلَيْهِ فَقَالُوا سَلَامًا قَالَ سَلَامٌ
قَوْمٌ مُنْكَرُونَ (٢٥) فَرَاغَ إِلَى أَهْلِهِ فَجَاءَ
بِعِجْلٍ سَمِينٍ (٢٦) فَقَرَّبَهُ إِلَيْهِمْ قَالَ أَلَا
تَأْكُلُونَ (٢٧)﴾ [سورة الذاريات].

“Shin, Labarin baƙin Ibrahim, waɗanda aka girmama, ya zo maka ?. A lokacin da suka shiga gare shi, sai suka yi sallama; ya ce “Aminci ya tabbata a gare ku, mutane baƙi !”. Sai ya juya zuwa ga Iyalansa, Sa’annan ya zo da maraƙi tutturna. Sai Ya kusantar da shi zuwa gare su, ya ce”. Ba za ku Ci ba ?”

[Suratul Zariyati : 24-27]

A wata surar kuma, Al-ƙur’ani ya tabbatar da cewa, matar mutum, da yace daga cikin Iyalinsa kuma ya ba ta sunan (Ahlul Baiti) in da ya ce, a kan matar Annabi Ibrahim (AS):

﴿وَامْرَأَتُهُ قَائِمَةٌ فَضَحِكَتْ فَبَشَّرْنَاهَا بِإِسْحَاقَ
وَمِنْ وَرَاءِ إِسْحَاقَ يَعْقُوبَ (٧١) قَالَتْ يَا
وَيْلَتَى أَأَلِدُ وَأَنَا عَجُوزٌ وَهَذَا بَعْلِي شَيْخًا إِنَّ
هَذَا لَشَيْءٌ عَجِيبٌ (٧٢) قَالُوا أَتَعْجَبِينَ مِنْ

أَمْرِ اللَّهِ رَحْمَةُ اللَّهِ وَبَرَكَاتُهُ عَلَيْكُمْ أَهْلَ الْبَيْتِ
إِنَّهُ حَمِيدٌ مَجِيدٌ (٧٣)﴾ [سورة هود]

"Kuma matarsa tana tsaye. Tayi dariya sai muka yi mata bushara (da haihuwar) Is'haƙa, kuma a bayan Is'haƙa, Yaƙuba. Sai ta ce, "ya kaitona ! shin zan haihu ne alhali kuwa ina tsohuwa, kuma ga mijina tsoho ne? Lalle wannan haƙiƙa, abu ne mai ban mamaki." Suka ce kina mamaki ne daga al'amarin Allah? Rahamar Allah da albarkarsa su tabbata a kanku, ya Ahlul Baiti (mutanen babban gida) ! Lalle ne shi abin godewa ne, mai girma."

[suratul Hud : 71 – 73]

Don haka, a lokacin da Manzon Allah (SAW) ya ke cewa: "mafi alherinku, shi ne, wanda ya fi kyautata wa iyalinsa. Ni kuwa ni ne zakara a cikinku ta wajen kyautata ma iyalina. Manzon Allah (SAW) ya na nuni ne

zuwa ga kyautatawar da ya ke yi wa matansa.

A kan haka, iyalin gidan Manzon Allah (SAW) ke nan, su ne matansa a matakin farko. Haka kuma malamai sun yi bayani bisa ga wasu hujjoji da zamu faɗe su nan gaba cewa, 'ya'yansa, zuri'arsa da makusantansa (danginsa) waɗanda aka haramta wa cin sadaka, saboda kusancinsu da shi, aka tanadar masu humusin humusin ganima (4/100) dukkansu suna cikin iyalan gidansa **(Ahlulbaiti)**.

Ba wata tantama akan kasancewar matan Manzon Allah a cikin iyalansa idan mu ka yi nazarin ayoyin da Allah ya kira **(Ahlulbaiti)** a cikinsu. Ga su nan mai karatu sai ka duba su da kyau:

﴿ يَا أَيُّهَا النَّبِيُّ قُلْ **لِأَزْوَاجِكَ** إِنْ كُنْتُنَّ تُرِدْنَ الْحَيَاةَ الدُّنْيَا وَزِينَتَهَا فَتَعَالَيْنَ أُمَتِّعْكُنَّ وَأُسَرِّحْكُنَّ سَرَاحًا جَمِيلًا (٢٨) وَإِنْ كُنْتُنَّ تُرِدْنَ اللَّهَ وَرَسُولَهُ وَالدَّارَ الْآخِرَةَ فَإِنَّ اللَّهَ أَعَدَّ لِلْمُحْسِنَاتِ مِنْكُنَّ أَجْرًا عَظِيمًا (٢٩) **يَا نِسَاءَ**

**النَّبِيِّ** مَنْ يَأْتِ مِنْكُنَّ بِفَاحِشَةٍ مُبَيِّنَةٍ يُضَاعَفْ
لَهَا الْعَذَابُ ضِعْفَيْنِ وَكَانَ ذَلِكَ عَلَى اللَّهِ يَسِيرًا
(٣٠) وَمَنْ يَقْنُتْ مِنْكُنَّ لِلَّهِ وَرَسُولِهِ وَتَعْمَلْ
صَالِحًا نُؤْتِهَا أَجْرَهَا مَرَّتَيْنِ وَأَعْتَدْنَا لَهَا رِزْقًا
كَرِيمًا (٣١) **يَا نِسَاءَ النَّبِيِّ** لَسْتُنَّ كَأَحَدٍ مِنَ
النِّسَاءِ إِنِ اتَّقَيْتُنَّ فَلَا تَخْضَعْنَ بِالْقَوْلِ فَيَطْمَعَ
الَّذِي فِي قَلْبِهِ مَرَضٌ وَقُلْنَ قَوْلًا مَعْرُوفًا (٣٢)
وَقَرْنَ فِي بُيُوتِكُنَّ وَلَا تَبَرَّجْنَ تَبَرُّجَ الْجَاهِلِيَّةِ
الْأُولَى وَأَقِمْنَ الصَّلَاةَ وَآتِينَ الزَّكَاةَ وَأَطِعْنَ
اللَّهَ وَرَسُولَهُ إِنَّمَا يُرِيدُ اللَّهُ لِيُذْهِبَ عَنْكُمُ
الرِّجْسَ **أَهْلَ الْبَيْتِ** وَيُطَهِّرَكُمْ تَطْهِيرًا (٣٣)
وَاذْكُرْنَ مَا يُتْلَى فِي بُيُوتِكُنَّ مِنْ آيَاتِ اللَّهِ
وَالْحِكْمَةِ إِنَّ اللَّهَ كَانَ لَطِيفًا خَبِيرًا (٣٤)﴾.
[سورة الأحزاب].

**“ya kai Annabi ! ka ce wa Matanka - , “Idan kun kasance**

kuna nufin rayuwar duniya da ƙawarta, to, ku zo in yi muku kyautar ban kwana, kuma in sake ku, saki mai kyau." Kuma idan kun kasance kuna nufin Allah da Manzonsa da gidan Lahira, to, Lalle, Allah ya yi tattalin wani sakamako mai girma ga masu kyautatawa, daga gare ku." Ya Mata nannabi ! wadda ta zo da alfasha bayyananna daga cikinku, za a ninka mata azaba ninki biyu. Kuma wancan ya kasance mai sauƙi ga Allah. Kuma wadda ta yi tawali'u daga cikinku ga Allah da Manzonsa, kuma ta aikata aiki na ƙwarai, za mu ba ta sakamakonta ninki biyu, kuma mun yi mata tattalin arziki na karimci. Ya mata nannabi! Ba ku zama kamar kowa ba daga mata, idan kun yi taƙawa, saboda haka kada ku sassautar da magana har wanda ke da cuta a cikin zuciyarsa ya yi ɗammani, kuma ku faɗi magana ta alheri. Kuma ku tabbata a cikin

> gidajenku, kuma kada ku yi fitar gaye-gaye irin fitar gaye-gaye ta jahiliyyar farko kuma ku tsai da sallah, kuma ku bayar da zakka, kuma ku yi ɗa'a ga Allah da Manzonsa. Allah na nufin ne kawai ya tafiyar da ƙazanta daga gare ku, ya (Ahlulbaiti) Mutanen Babban Gida! kuma ya tsarkake ku, tsarkakewa. Kuma ku tuna abinda ake karantawa a cikin ɗakunanku daga ayoyin Allah da hukunci. Lalle Allah ya kasance mai tausasawa.
>
> [suratul Ahzab : 28 – 34]

Manzon Allah da kansa ya kan kira matansa da sunan **(Ahlulbaiti)** kamar yadda za mu gani a cikin wannan Hadisi da Imamul Buhari ya ruwaito.

Daga Anas ɗan Malik (R.A) ya ce, Wata rana Manzon Allah (SAW) ya shiga ɗakin Sayyida A'ishah, bayan ya yi biko da matarsa Zainab 'yar Jahshi, sai ya ce: Amincin Allah da rahamarsa su tabbata gare ku, ya ku **(Ahlulbaiti)** "mutanen Babban

Gida". Ta karɓa masa, ita A'ishahr, da cewa "ku ma amincin Allah da rahamarsa da albarkarsa su tabbata gare ku, ya kwanan amarya? Allah ya sa alheri". Sa'annan sai ya ci gaba da lelleƙa ɗakunan matansa, suna gaisuwa kamar yadda suka gaisa da sayyidah A'ishah (RA) yana faɗa ma su abin da ya faɗa mata, su kuma su na amsa ma sa kamar yadda ta amsa ma sa.[1]

Haka kuma, gaba ɗayan zuri'ar Manzon Allah (SAW) na daga cikin iyalansa. Za mu fahimci haka idan muka dubi Salatin Ibrahimiyyah wanda Manzon Allah ya koyar da Sahabbansa, ya na cewa:

اللهم صل على محمد وعلى أزواجه وذريته كما صليت على

إبراهيم

وبارك على محمد وعلى أزواجه وذريته كما باركت على إبراهيم

إنك حميد مجيد

---

[1] Sahihul Bukhari, Kitabul Tafsir, Babin "kada ku shiga gidan Annabi sai an yi muku izni", Hadisi na 4793.

"ku ce ya Ubangiji ka daɗa tsira bisa ga Muhammadu da matansa da Zuri'arsa, kamar yadda ka daɗa tsira bisa ga Ibrahim. Ka kuma yi albarka bisa ga Muhammadu da Matansa da Zuri'arsa, kamar yadda ka yi albarka bisa ga Ibrahim, Lalle kai ne Mai girma, abin godiya".[2] Wannan ya zo ne, a matsayin fassara ga abinda ya zo a ruwayar da tafi shahara kamar haka:

اللهم صل على محمد وعلى آل محمد

"Allahuma Salli Ala Muhammadin Wa Ala Ali Muhammadin…".

Dangin Manzon Allah waɗanda ke shiga a cikin **Ahlulbaiti** sun haɗa da duk jinsin mutanen da Manzon Allah ya haramta ma su cin sadaƙa saboda sun yi tarayya da shi a kakansa Abdul Muɗɗalib, kuma sun haɗa da; Iyalin Aliyu da na jafaru da na Aƙilu da na Abbas kamar yadda yazo a ruwayar Zaidu bin Arƙam a cikin Sahihu Muslim.[3] Wasu malamai ma sun sanya

---

[2] Sahihul Bukhari, Hadisi na 3369 da Sahihu Muslim, Hadisi na 407.

[3] Sahihu Muslim, Hadisi na 2408

iyalan Harisu ɗan Abdul-muɗallibi. Ga nasu dalilin:

An ruwaito cewa, Abdul-Muɗɗalibi ɗan Rabiatu ɗan Abbas ɗan Abdul-Muɗɗalibi, da Falalu ɗan Abbas ɗan Abdul Muɗɗalibi sun nemi Manzon Allah (SAW) su biyu, da ya ɗauke su aikin karɓar Zakka domin su samu kamishon da ake bai wa masu karɓarta daga cikinta. Sai Manzon Allah (SAW) ya ce ma su: "Wannan Zakka da kuke gani, ƙazantar mutane ce, ba ta halatta ga Muhammadu da Iyalin gidansa.[4] Wannan ya na ingantar da zaman Iyalan Harisu daga **Ahlulbaiti**, don shi ma ɗa ne ga Abdulmuɗɗalib.

Wannan da'irar tana daɗa faɗi idan muka leƙa wasu nassoshin, kamar ruwayar da Ɗabarani da Haisami su ka kawo a littafansu cewa, a lokacin da wasu mata suka yi wa Durratu 'yar Abu Lahabi ɗan Abdul Muɗɗalibi gorin cewa, Hijirarta, ba za ta amfane ta da komai ba, don Allah (SWT) ya yi tir da mahaifinta a cikin Al-ƙur'ani, Manzon Allah (SAW) ya sami wannan labari, sai ya ƙulla huɗuba. A cikinta kuma

---

[4] Sahihu Muslim, Hadisi na 1072.

yake cewa; A kan me za a cuta min ga ɗaya daga cikin Iyalaina, a yi mata gori?.[5]

Bisa ga haka ne, Malam Abbad ya ce: Duk musulmin da ya yi tarayya da Manzon Allah (SAW) a wajen kakansa Abdul Muɗɗalib to, yana cikin **Ahlulbaiti** kuma cin sadaka ya haramta gare shi.[6]

### 1.2 'Yan'uwan Haihuwar mahaifin Manzon Allah (SAW) Maza da Mata

Waɗannan sun haɗa da 'ya'yan ɗakuna daban daban kamar haka:-

1- **Harisu**: Shi ne babbansu, da shi ne kuma ake yi wa Abu Ɗalib alkunya. Mahaifiyarsa ita ce Safiyyatu 'yar Junaidibu.

2- Yan'uwan mahaifin Manzon Allah (SAW) na uwa ɗaya uba ɗaya, guda biyar, da suka haɗa da: **Zubairu** da

[5] Al 'Mu'jamul Kabir, na Ɗabarani (24/259) da Majmau'l Zawa'id, na Haisami (9/258).

[6] Fadlu Ahlil Baiti Wa Uluwwu Makanatihim inda Ahlils Suuna, Na Abdul Muhsin bin Hamad al-Abbad al Badr, shafi na 11.

**Abu-Ɗalib** da **Arwa** da **Atika** da **Ummu Hakim al-Baidha'u** (tagwan Abdullahi). Mahaifiyarsu itace Faɗimatu 'yar Amru Al-makhzumiyya.
3- **Hamza** da **Muƙawwamu** da **Safiyyatu**. Mahaifiyarsu ita ce Halatu 'yar Wahabi, wato da ita da Mahaifiyar Manzon Allah (SAW) ɗiyan wa da ƙanwa ne.
4- **Abbas** da **Darraru**. Mahaifiyarsu ita ce Nutailatu 'yar Janabizu.
5- **Abu Lahabi**. Sunansa na yanka shi ne Abdul-Uzza. Mahaifiyarsa ita ce Lubna 'yar Hijru Al-khuzaimiyyah.

Akwai kuma irin su Abdul-Ka'abati da Hajlu da Kusamu da Gaidaƙu a cikin wannan ayari, amma a ɗan wannan bincike ba mu kai ga sanin iyayensu mata ba.

Huɗu daga cikin waɗannan 'yan'uwa, na mahaifin Manzo Allah (SAW) ne, suka

riski Musulunci, daga cikin maza. Wato; Hamza da Abbas da Abu-Ɗalib da Abu-Lahabi. Daga cikin mata kuma akwai guda uku. Wato; Safiyyatu da Arwa da Atika. Kuma matan gaba ɗaya sun musulunta; mazan kuwa sai aka yi raba dai dai, biyu suka ba da gaskiya, wato Hamza da Abbas (RA), biyu kuwa suka cije, wato; Abu-Ɗalib da Abu-Lahab. Banbancin da ke tsakaninsu kawai, shi ne, rashin bayar da gaskiyarsu bai hana, Abu-Ɗalib ya ba Manzon Allah (SAW) gagarumar gudammawa ba. saɓanin Abu-Lahabi, wanda ba shi ga maciji da Manzon Allah (SAW).

Sauran kuwa da ba su riski Musuluncin ba, sun haɗa da : Harisu da Zubairu da Umaimatu da Ummu Hakim Al-Baidha'u da Barratu.

### 1.3 'Ya'yan 'yan'uwan mahaifin Manzon Allah (SAW).

Babu abinda ya yi saura, daga cikin Zuri'ar Zubairu da Hamza. Amma Harisu da Abbas da Abu-Ɗalib da Abu-Lahabi duk zuri'arsu ta wanzu.

**‘Ya’yan Hamza:** Hamza ya haifi ‘ya’ya takwas (8) biyar (5) Maza, da suka haɗa da : Ya’ala da Ammaru da Umaru da Amiru sai Uku (3) Mata; Ummul-Fadhli da faɗimatu da Umamatu.

Babban ɗan Hamza, Ya’ala ne kawai ya rayu, har ya haifi ‘ya’ya Maza guda biyar (5) waɗanda kuma Allah bai yi wa tsawon kwanukka ba.

**‘Ya’yan Abbas:** Abbas ya haifi ‘ya’ya goma sha Huɗu (14) goma (10) maza, huɗu (4) Mata. Sun haɗa da; Fadhlu da Abdullahi da Kusamu su ne manyan ‘ya’yansa, da Ubaidullahi da Ma’abad da Abdurrahman. Mahaifiyarsu ita ce, Ummul Fadhli, Lubabatul-Kubra, (yar Ummul-Muminina Maimunatu ‘yar Harisu,) Al-Hilaliyyah. Wadda ke da ‘yar ’uwa mai suna, Lubabatus-Sugra, mahaifiyar Khalidu ɗan Walidu. Sai kuma Harisu da Kusamu da Aunu da Tammam, su kuwa mahaifiyarsu Barumiya ce (wadda aka zo da ita daga ƙasar Rum). Duk waɗannan ‘ya’ya na Abbas sun sadu da Manzon Allah (SAW). Har babbansu ma da mai bi masa, sun ruwaito Hadissai daga Manzo kai tsaye. Na

biyun ma shi ne Manzon Allah (SAW) ya yi wa addu'ar laƙantar Al-ƙur'ani da Tafsiri. Shi ne kuma kakan halifofi Abbasiyyawa. Matan kuwa su ne; Ummu Habib da Aminatu da Safiyyatu da Ummul – Fadhli.

**'Ya'yan Abu-Ɗalib:** Abu-Ɗalib shi ya haifi Aliyu da Ja'afaru da Aƙilu da Jumanah da Ummu Hani'i, zanannen sunanta kuwa shi ne Fakhitah. Mahaifiyarsu ita ce Faɗimatu 'yar Asad ɗan Hashimu. Ta kuma riski Manzon Allah (SAW).

**'Ya'yan Abu Lahabi:** Ya haifi Durratu wacce labarinta ya gabata.

**'Ya'yan Safiyyatu:** Ita kuma Safiyyatu 'yar Abdul-Muɗɗalibi, ita ce mahaifiyar Zubairu ɗan Auwamu, ɗayan waɗanda aka yi wa bushara da Aljanna. Zubairu kuwa shi ne wanda ya Auri Asma'u 'yar Sayyadi Abubakar as-Siddiƙu, suka haifi Abdullahi ɗan Zubairu, wanda yake shi da baban nasa da Umminsa da babanta da kakanta duk, Sahabbai ne (RA). Daga cikin 'ya'yan Safiyyatu kuma akwai As-Sa'ibul – Badri.

**'ya'yan Umaimatu:** An yi saɓani a cikin, riskuwarta ga musulunci. Amma 'ya'yanta guda shidda (6), duk sun musulunta babu

shakka. Uku daga cikinsu maza ne; Shahidu, Abdullahi Al-Mujada' da Muhajiru, Abdullahi, Abu Ahmad al'A'ama da Ubaidullahi ɗan Jahshu mijin Ramlatu na farko kafin Manzon Allah (SAW) ya aure ta. Uku kuwa mata ne waɗanda kuma suka musulunta da wuri har su ka yi hijira sau biyu. Su ne; Zainab Ummul-Muminina da Hamnatu da Ummu Habibah.

**'ya'yan Arwa:** Ita kuma Arwa ita ce mahaifiyar Ɗulaibu ɗan Umaru, wanda ya na daga cikin Sahabai.

**'ya'yan Atika:** Atika ta auri Abu-Ummayyah ɗan Magirata Al-makhzumi, suka haifi ; Abdullahi da zubairu da Ummul-Mumunina, Ummu Salamah.

**'ya'yan Barratu:** Ita kuma Barratu ita ta haifi Abu Salamah (RA) mijin Ummu Salamah kafin ya rasu Manzon Allah (SAW) ya aure ta. Haka kuma ita ta haifi sahabi Abu Sabrata.

**'ya'yan Ummu hakim, Al-Baidha'u:** ita ce tagwan mahaifin Manzon Allah (SAW) wadda aka haife su rana ɗaya da shi. Ita ce kuma Kakar Sayyiduna Usman ɗan Affana

(RA) mahaifiyar uwarsa Arwa ɗiyar kuraizu.

**Mu kula:**

Daga abin da ya gabata, muna iya lura cewa,

- Iyayen Mummunai Ummu Salamah (ɗiyar Atika) da Zainab ‘yar Jahshu (ɗiyar Umaimatu) duk taubashinnen Manzon Allah (SAW) ne, (ɗan macce da ɗan namiji) ‘ya’yan gwaggwanninsa.
- Ali ɗan Abu ɗalib a matsayin ƙanen Manzon Allah (SAW) ne, domin da mahaifinsa da na Manzon Allah (SAW) wa da ƙani ne. Ita kuma Fatimah, matarsa, a matsayin ‘ya ta ke a wurinsa.
- Sayyiduna Usman (RA) a matsayin ɗa yake ga Manzon Allah (SAW), domin jikan gwaggonsa ne. Daga nan za mu fahimci cewa, ‘ya’yan Manzon Allah (SAW) da ya aura Ruƙayyah da Ummu Kulsum, a matsayin ƙannensa ne na zumunta.
- Uwar gidan Baffan Manzon Allah (SAW), Abbas ɗan Abdul Muɗɗalibi,

ina nufin Lubabatul Kubra yar Matar Manzon Allah (SAW) ce Maimunatu ‘yar Harisu.

- Shi kuma Khalid ɗan Walid (RA) ɗa ne ga Manzon Allah (SAW) ta wajen Uwar Mummunai Maimunatu, domin ƙanwar uwarsa ce.
- Ummu Hani’i (RA) wadda Manzon Allah (SAW) ya ke ziyarta a Ajyad, har ma wasu ruwayoyi su ka nuna cewa, daga gidanta ne aka yi Isra’i da shi, a matsayin ƙanwarsa ta ke, ‘yar baffansa, Abu ɗalib, kuma yar Sayyiduna Ali (RA).
- Abdullahi ɗan Abbas da ƙanensa Fadlu duk da yake ƙannen Manzon Allah (SAW) ne ta wajen mahaifinsu, amma kuma ‘ya’yansa ne ta wajen matarsa Maimunatu, ƙanwar mahaifiyarsu.
- Abu Salamah (RA) wanda Manzon Allah (SAW) ya auri matarsa a bayan rasuwarsa Ummu Salamah, a matsayin ƙanin Manzon Allah (SAW) ya ke, ɗan gwaggonsa Barratu.

- Haka shi ma Ubaidullahi ɗan Jahshu, wanda Manzon Allah (SAW) ya auri matarsa Ramlatu a bayan rasuwarsa, taubashin Manzon Allah (SAW) ne, ɗan gwaggonsa Umaimatu. Haka kuma shi ne wan matarsa Zainab ɗiyar Jahshu.
- Zubairu ɗan Awwamu wanda ya auri Asma'u ɗiyar Sayyiduna Abubakar kuma yar matar Manzon Allah (SAW) A'ishah, shi ma taubashin Manzon Allah (SAW) ne, ɗan gwaggonsa Safiyyatu.

## 1.4 Kawunnen Manzon Allah (SAW) ('Yan'uwan haihuwar Mahaifiyarsa):

Aminatu ɗiyar Wahabu, mahaifiyar Manzon Allah (SAW) na da 'yan uwan haihuwa guda biyar (5) Maza, da suka haɗa da:

1- Al Aswadu ɗan Wahabu, ya musulunta, ya abokanci Manzon Allah (SAW), ya

kuma ruwaito Hadisai daga gare shi.

2- Abdullahi ɗan wahabu: ya musulunta ranar da aka ci garin Makkah.
3- Umaru ɗan Wahabu: Ba cikakken labarinsa.
4- Abdu Yagusa ɗan Wahabu: Shi ne mafi shahara daga cikin kawunnen Manzon Allah (SAW). Bai riski Manzanci ba. Daga cikin zuri'arsa, akwai Al-Aswad ɗan Abdu Yagusa – ya mutu mushiriki, yana kuma mai tsananin tozartawa ga Manzon Allah (SAW). Sai dai ya haifi 'ya'ya Musulmai, waɗanda su ka abokanci Manzon Allah (SAW)

su ne; Abdurrahman da Khalidatu. Haka kuma ya na da ɗa mushriki mai suna, Arƙamu ɗan Abdu yagusa, shi kuma wannan yana da ɗa mai suna Abdullahi ɗan Arƙamu, wanda ya musulunta, ya abokanci Manzon Allah (SAW).

5- Khalafu ɗan Wahabu: Yana da ɗa mai suna Al-Aswadu ɗan khalafu, sahabi ne, kuma ya yo ruwaya daga Manzon Allah (SAW).

Haka kuma Amina tana da 'yan'uwan haihuwa mata, guda huɗu (4) da suka haɗa da:

1- Fakhita 'yar Amiru
2- Furai'atu 'yar Wahabu

3- Uƙailatu 'yar kumainu
4- Ummu Abdin, mahaifiyar Abdullahi ɗan Mas'ud

Tabbataciyar magana dai ita ce, dukan matan nan, danginta ne daga ƙabilar Bani Zuhrah dangin mahaifinta, amma ba abokan haihuwarta ba ne. Sai fa Uƙailatu 'yar kumainu, ita kam, 'yar'uwar Aminatu ce ta wajen uwa, amma ba su haɗa uba ba. Akan haka, ita ce Inna ta ainihi ga Manzon Allah (SAW).

## 1.5 Matan Manzon Allah (R.A)

Manzon Allah (SAW) ya auri mata goma sha ɗaya (11) a rayuwarsa.

1- Khadijatu 'yar Khuwailidu ɗan Asadu ɗan Abdul-Uzza ɗan Kusayyu: Macce ta farko a Musulunci, Uwar gidan Manzon Allah (SAW), Uwar 'ya'yansa gaba ɗaya in ban da ɗan autansa Ibrahim.

‘Yar uwarsa ce ga zumunta, domin Kusayyu, kakanta na uku shi ne kakansa na huɗu. Ta rayu tare da Manzon Allah (SAW), ita kaɗai, a matsayin matarsa, tsawon shekaru ashirin da biyar (25), bai yi ma ta kishiya ba har Allah ya cika ajalinta. Ta taimaka ma Manzon Allah (SAW) matuƙa, kuma ya kasance ya na daranjanta ta, ya na yaba ma ta. Kuma a lokacin da ta rasu ya yi baƙin ciki ainun, sannan ya kasance ya na kyautata ma aminnanta a bayan rasuwarta.

2- Saudatu ‘yar Zam’atu: Ita ce amaryar Manzon Allah (SAW) ta farko bayan rasuwar uwargidansa Khadijah, ta zauna tare da shi tsawon shekara Uku (3), ita kaɗai. Da ya ke Saudatu dattijuwa ce, daga baya sai ta yafewa Nana A’ishah kwananta a wurin Manzon Allah (SAW), don ta san zai yi farin ciki da haka, ta na neman yardarsa.

3- A’ishatu ‘yar Abubakar Siddiƙu : Manzon Allah (SAW) ya

auri Sayyada A’ishah, a cikin watan Shawwal, shekara ta tara (9), bayan da Allah ya nuna masa wannan auren a cikin mafarki in da ya ga Jibrilu (AS) ɗauke da ita A’ishahr a cikin wani kyakkawan ƙyalle na alhariri, ya na ce masa: ga matarka. Nana A’ishah ta ci gaba da zama tare da Saudatu wasu tsawon shekaru uku kafin Manzon Allah (SAW) ya auri Hafsah ‘yar Umar. Ita kaɗai ce budurwa daga cikin matansa kuma ya kasance, ya na matuƙar ƙaunarta fiye da sauran matansa. A dalilin haka ne munafukai su ka shirya ma ta ƙarya, sai alƙur’ani ya sauko daga wurin Allah ya na wanke ta.[7] Ta yaɗa ilmi mai tarin yawa da albarka a cikin shekaru kusan hamsin (50) da ta yi bayan Manzon Allah (SAW).

4- Hafsatu ‘yar Umar ɗan Khaɗɗabi: Manzon Allah ya aure ta, a cikin shekara ta Uku (3) bayan hijira. Kamar yadda ta ke bi ma Nana A’ishah ga auren Manzon Allah

[7] Duba Suratun Nur: Daga aya ta 11 zuwa ta 20.

(SAW), haka ma it ace ta ke takara da ita, a wajen farin jininta da ƙuruciya.

5- Zainab ‘yar Khuzaimah al-Hilaliyyah: Ita ce ake yi wa laƙabi da Uwar talakawa, saboda yawan sadakarta. Manzon Allah (SAW) ya aure ta, da wata biyu ko Uku, Allah ya yi mata rasuwa.

6- Ummu Salamata, Hindu ‘yar Umayyata, Baƙuraisha ce, Makhzumiyyah. Ita ce wadda ta ga Manzon Allah tare da Mala’ika Jibirilu, shi Jibirilun yana cikin siffar wani kyakkyawan saurayi daga cikin sahabbai ana kiransa Dihyatu. Ta na daga cikin mata masu hankali da ilmi. Ita ce ma ta lurar da Manzon Allah (SAW) game da wata dabara da zai jawo hankalin Sahabbansa a ranar hudaibiyyah, kuma dabarar ta ci nasara sosai, ta kuɓutar da musulmi daga faɗawa cikn hushin Allah da manzonsa.

7- Zainab ‘yar Jahshu ‘yar Umaimatu ‘yar Abdul Muɗɗalibi. Allah (SWT) ne ya shirya aure

tsakaninta da Manzon Allah (SAW) a shekara ta uku ko kuma ta biyar bayan Hijira. Kuma Allah ya ɗaura auren, ya ba da shelar haka cikin alƙur'ani.[8] Annabi kuwa ya yi mata walima ƙasaitacciya. Ta na da saurin fushi da saurin hucewa. Duk ta fi matan nannabi (SAW) yawan ƙasƙantar da kai ga Allah da yawan ayukkan neman lada bisa ga shedar kishiyarta Nana A'ishah.

8- Juwairiyyatu 'yar Harisu: Manzon Allah (SAW) ya aure ta bayan yaƙin da ake kira Muraisi'u, a cikin shekara ta biyar ko shida, bayan hijira. Kuma a sanadiyyarta ne musulmi suka 'yanta bayi ɗari, daga ƙabilarsu ta Banul Musɗalaƙ, su kuma a dalilin haka duk su ka musulunta.

9- Ummu Habibah 'yar Abu-Sufyana (Sarkin Makka). Sunanta na yanka shi ne; Ramlatu. Tana kuma daga cikin matan farko da suka yi hijira zuwa Habasha, in da

---

[8] A Suratul Ahzabi, aya ta: 38.

mijinta ya rasu ya na musulmi.[9] Sa'annan Manzon Allah (SAW) ya aure ta. Ta kasance mai yawan tsentseni da ibada da girmama Manzon Allah (SAW). A lokacin halifancinsa, ƙanenta Mu'awiyah ya kasance ya na matuƙar darajanta ta, don haka ne ma ake ce masa "kawun Mummunai" saboda 'yar uwarsa uwar Mummunai ce da nassin alƙur'ani.

10- Safiyyatu 'yar Huyaiyu: Manzon Allah (SAW) ya aure ta, a cikin shekara ta shida bayan hijira. Kuma tana daga cikin zuri'ar Haruna ɗan Imrana, ɗan'uwan Annabi musa (AS). Mace ce mai haƙuri na natsuwa matuƙa. Daga aurenta ne aka samu hukuncin namiji ya 'yanta kuyangarsa, kuma yace ita ɗin kanta

---

[9] Bincike ya tabbatar da rashin ingancin bayanan da ke cewa, Ubaidullahi ɗan Jahshu ya yi ridda ne bayan da su kayi hijira tare da matarsa Ummu Habiba zuwa Habasha. Duba Muƙalar da Muhammad bin Abdillahi al Uwaishin ya rubuta a cikin Mujallar **al Bayan** ta 182, wadda ta fito a watan Shawwal 1423B.H./Dasumba 2002M. Daga shafi na 22.

ce sadakin aurenta. Haka ne ita ya yi wa Juwairiyyah.

11- Maimunatu ‘yar Harisu Al-Hilaliyyah: ita ce ‘yar autan matan Manzon Allah (SAW). Ya aure ta ne a cikin shekara ta bakwai bayan hijira, ya yi biko da ita a wani wuri da ake kira “Sarfu” lokacin da ya ke tafiya don ramka Umrarsa da bai samu yi ba a lokacin Hudaibiyyah. Nana A’ishah ta ba da sheda akanta ta na cewa, duk ta fi mu taƙwa da kuma sada zumunta.

## 1.6 ‘Ya’yan Manzon Allah (SAW) da jikokinsa maza da mata:

Manzon Allah (SAW) ya haifi ‘ya’ya bakwai (7) Uku Maza, da suka haɗa da:-

1. **Al-ƙasim:** Shi ne ɗan farin, kuma da shi ne ake yi wa Manzon Allah (SAW) alkunya.
2. **Abdullahi:** (ana yi ma sa laƙubba biyu:

Aɗɗayibu da Aɗɗahiru)

3. **Ibrahim**: shi ne ɗan autan Manzon Allah (SAW).

Sai huɗu (4) mata, da suka haɗa da:

4. **Zainab:** Ita ce babba a cikin mata. Ta auri Abul Asi ɗan Rabi'u daga ƙabilar Banu Umayyah, waɗanda sun haɗa zuri'a da Manzon Allah (SAW) a kakansa Murratu ɗan Ka'abu.
5. **Ruƙayyatu:** Ta auri Sayyiduna Usman (RA), Shugaban ƙabilar Banu

Umayyah a lokacinsa. Ta rasu wajen naƙudar ɗanta Abdullahi, a daidai lokacin da su ka fita tare da mijinta wajen yaƙin Badr. Wannan ma shi ne daliln da ya sa Sayyiduna Usman bai samu yaƙin Badr ba, domin jinyarta a hanya. Amma Annabi (SAW) ya raba ganimar da shi, abin da ya ke nuna sun samu ladar yaƙin da shi da matarsa.

6. **Ummu Kulsum**: Ta auri mijin yarta Sayyiduna Usman, daga ƙabilar Banu Umayyah. Amma ba su samu haifuwa ba, har ita ma Allah ya karɓi rayuwarta.
7. **Faɗimatu:** ita ce ‘yar autar ɗakinsu, kuma mai bi ma ɗan autan gidan bakin ɗaya, shi ne Ibrahim. Ta auri wanta Aliyu ɗan Abu ɗalib a ƙarshen shekara ta biyu, ta haifi ‘ya’ya biyar da shi kamar yadda za

mu faɗa a nan
gaba kaɗan.

Allah (SWT) ya ambaci waɗannan 'ya'ya mata na Manzon Allah, a ɗunƙule, inda ya ce:

﴿يَا أَيُّهَا النَّبِيُّ قُلْ
لِأَزْوَاجِكَ وَبَنَاتِكَ وَنِسَاءِ
الْمُؤْمِنِينَ يُدْنِينَ عَلَيْهِنَّ مِنْ
جَلَابِيبِهِنَّ ذَلِكَ أَدْنَى أَنْ
يُعْرَفْنَ فَلَا يُؤْذَيْنَ وَكَانَ اللَّهُ
غَفُورًا رَحِيمًا (٥٩)﴾
[سورة الأحزاب].

**(ya kai Annabi ! ka ce wa mata naurenka da 'ya'yanka mata, da matan muminnai su kusantar da ƙasa daga manyan**

tufafin da ke a kansu. Wancan ya fi sauƙi ga a gane su domin kada a cuce su. Kuma Allah ya kasance mai gafara mai jinƙai)

[Suratul Ahzab : 59]

Waɗannan 'ya'ya na Manzon Allah (SAW) guda bakwai, duk Sayyidah Khadijatu ce ta haife su, sai fa Ibrahim, wanda mahaifiyarsa ita ce; Mariyah al-ƙibdɗiyyah. Uku daga cikin 'ya'yan Manzon Allah (SAW) ɗin nan, mata, wato; Faɗimatu da Zainab da Ruƙayyah sun kai fagen yin aure da haihuwa.

(a) Faɗimatu 'yar Manzon Allah (SAW) ta haifi:-

1. Hassan(Ya haifi zuri'a mai yawa)
2. Hussaini(Shi ma zuri'arsa ta yaɗu)

3. Muhsinu (ya rasu yana ƙarami sosai)
4. Ummu Kulsum, wadda ta auri Sayyiduna Umar ta Haifa ma sa; Zaidu da Ruƙayyah.[10] Bayan da ya rasu sai ta auri 'ya'yan Amminta guda uku; Aunu da Muhammadu da Abdullahi 'ya'yan Ja'afaru ɗan Abu ɗalib, ɗaya bayan ɗaya, ƙarshe ta rasu hannun Abdullahi ɗan Ja'afaru sai kuma aka ba shi 'yar'uwarta

10 Zaidu ya girma, ya je Hunain, wurin da aka taɓa yaƙi a zamanin Manzon Allah (SAW) ya gamu da ajalinsa ta hannun Khalid ɗan Aslam, bawan mahaifinsa wanda ya jefe shi da mashi akan kuskure, kuma Allah ya yi masa cikawa a rana ɗaya da mahaifiyarsa. Ɗan Uwansa Abdullahi ɗan Umar ya yi masu sallah tare da iznin Sarkin Musulmi na wannan lokaci Al Hassan ɗan Ali. Ita kuma Ruƙayyah ta girma har ta auri wani mutum mai suna Ibrahim ɗan Nu'aimu An Nahham. Allah ya yi mata cikawa ba tare da ta samu zuri'a ba. Duba: *Sibɗun Nujumil Awali Fi Amba'il Awa'ili Wat Tawali* na Al Isami a alwarraƙ.com (1/224).

Zainab, suka haifi 'ya'ya da dama.

5. Zainab – al Kubra (wadda mu ka faɗa a sama).

(b) Zainab 'yar Manzon Allah (SAW) ta haifi:-

1. Aliyu, da
2. Umamatu: Mahaifinsu shi ne Abul Asi ɗan Rabi'u daga ƙabilar Banu Umayyah. Umamatu ƙarama ce a zamanin Manzon Allah (SAW), ya kan ɗauke ta idan ya na sallah. A lokacin rasuwar Nana Faɗimatu ne ta yi wa mijinta Sayyiduna Ali nuni da auren Umamatu ɗiyar yarta. Hakan kuma aka yi. Shi kuma a lokacin rasuwarsa sai ya yi ma ta nuni da ta auri ɗan uwansu Mugiratu ɗan Naufalu ɗan Harisu ɗan Abdul-Muɗɗalibi, kuma hakan aka yi. Ta haifu da shi amma

zuri'arsu ta ƙare, bat a yaɗu ta.

(c) Ruƙayyatu 'yar Manzon Allah (SAW) ta haifi :-

1. abdullahi ɗan Usman ɗan Affan (ya rasu yana ƙarami sosai)

Wannan shi ne bayanin waɗanda **Ahlulbaiti** su ka ƙunsa a wurin Ahlus Sunnah. To, a wurin Rafilawa abin ya banbanta, domin kuwa **Ahlulbaiti** a wurinsu su ne, mutanen kisa'u kawai. Sun kuma yi ittifaƙi a kan cewa matan Manzon Allah (SAW) ba su daga cikin **Ahlulbaiti.**[11]

Hujjar Rafilawa, a kan wannan matsayi, ita ce faɗar Allah (SWT)

﴿ قُلْ لَا أَسْأَلُكُمْ عَلَيْهِ أَجْرًا إِلَّا الْمَوَدَّةَ فِي الْقُرْبَى ﴾

(الشورى:٢٣).

[11] Duba Tafsirin al-Kummi, 2/192.

**“Kace, “ Ba ni tambayarku wata ijara a kansa, face dai soyayya ta cikin zumunta” [Surar shura : 23].**

Su kace, wai an tambayi Annabi (SAW) ma’anar wannan aya! sai ya ce Allah na nufin: Aliyu (RA) da Faɗimatu ne, da ‘ya’yansu Hassan da Hussaini.

A fili ya ke cewa, sun kauce ma gaskiya, domin kuwa wannan aya tana cikin Suratus Shura ne, wadda ta sauka a Makka kamar yadda tarayyar masana asirin saukar surorin Al-ƙur’ani suka tabbatar,[12] kafin zancen auren Ali da Faɗimatu, ballantana haifuwar Hassan da Hussaini. To, ta yaya Manzon Allah (SAW) zai fassara waccan aya, da cewa tana nufin son Al-Hassan da Al-Hussaini, alhali ba’a ko yi auren mahaifansu ba ballantana a haife su?!

Ɗan Abbas, shahararren masanin al-ƙur’ani wanda kuma ya fi gaba ɗayan **Ahlulbaiti** Ilmi, sai fa Ali (RA) ya fassara wannan aya da cewa: zumuncin da Allah ke nufi a cikin ayar, shi ne gaba ɗayan dangin

[12] Duba alal Misali: Tafsirin al-Bagwi 4/119.

Annabi (SAW) kuma babu wani gida daga cikin gidajen ƙuraishawa face Manzon Allah (SAW) na da dangantaka da su ta wajen wasu kakanninsa. Saboda haka ne ma, Ibnu Taimiyya ya hukuntar da zaman wancan Hadisi, da suka kafa hujja da shi, zuƙi ta mallau.[13] Haka ma Ibnu Hajar ya raunana shi.[14]

Haka nan kuma daga cikin hujjojinsu akwai ayar mubahala, wadda a cikinta Allah (SWT) ya ke cewa :

﴿ فَمَنْ حَاجَّكَ فِيهِ مِنْ بَعْدِ مَا جَاءَكَ مِنَ الْعِلْمِ فَقُلْ تَعَالَوْا نَدْعُ أَبْنَاءَنَا وَأَبْنَاءَكُمْ وَنِسَاءَنَا وَنِسَاءَكُمْ وَأَنْفُسَنَا وَأَنْفُسَكُمْ ثُمَّ نَبْتَهِلْ فَنَجْعَلْ لَعْنَةَ اللَّهِ عَلَى الْكَاذِبِينَ(٦١)﴾[آل عمران].

**"To, wanda ya yi musu da kai a cikinsa, a bayan abinda ya zo maka daga ilmi, to ka ce : "ku**

---

[13] Minhajus Sunnatin Nabawiyyah 7/99

[14] Fathul Bari :8/564

zo mu kirayi ‘ya’yanmu da ‘ya’yanku da matanmu da matanku da mu kanmu da ku kanku, sa’annan kuma mu sanya la’anar Allah a kan maƙaryata”. [Surar Ali Imrana : 61]

Su ka ce tun da ya ke, a lokacin da Allah ya saukar da wannan aya ya na umurnin Manzonsa da ya yi mubahala da kafirai, ya kawo danginsa su kawo nasu, ba’a ga Manzon Allah (SAW) ya kira kowa ba sai Ali da Matarsa da ‘ya’yansa. Wannan ya nuna kenan ba shi da wasu dangi in ba su ba.

To, amma kuma ai ayar ta faɗi da matanmu da matanku. Gaskiyar magana ita ce, ana nufin ya kira makusantansa, kuma ba lallai sai dukkansu ba. Don haka ne sai manzon Allah (SAW) ya gayyato Ali daga cikin danginsa Maza, Ya kira Faɗimatu daga cikin mata, Ya kira Hassan da Hussaini daga cikin ‘ya’ya. To, wane ne ya ce, wanda ba’a kira a rannan ba an kore shi daga cikn dangin Manzon Allah (SAW) da makusantansa,

kuma har matansa ba iyalansa ba ne tun da bai kira su ba?

Sauran 'ya'yan Manzon Allah (SAW) su shida (6), da zuri'arsu, da matansa goma sha ɗaya (11) da muka lisafa duk 'yan shi'a sun kore su daga zama **Ahlulbaiti**.

Daga 'ya'yan Ali da Fatima kuma, sun zaɓi kawai Hassan da Hussaini.[15].Haka ma zuri'ar Hassan ba su cikin **Ahlulbaiti** a wurinsu. Amma sun ɗan sassafta a cikin 'ya'yan Hussaini. Sun yarda da cewa, mutum tara (9) daga cikinsu reshe ne, daga itaciyar iyalan gidan Manzon Allah (SAW).

---

[15] Nana Fatima ta Haifa ma Ali 'ya'ya biyar kamar yadda muka gabatar. Shi kuma a aurarrakinsa bayan rasuwarta ya samu wasu 'ya'ya goma sha biyu (12) maza, da wasu goma sha shida (16) mata. Jimillar 'ya'yansa in aka haɗa da na Faɗimatu 33, maza goma sha biyar(15), mata goma sha takwas (18). Duba cikakken bayaninsu a littafin: al Riyadul Mustaɗaba Fi Jumlati man rawa fis Sahihaini minas Sahaba, na Amiri. Shafi na 180. Sai dai daga cikin 'ya'yan na Ali, biyar ne kawai zuri'arsu ta yaɗu, su ne; Hassan da Hussaini da Muhammad (wanda aka fi sani da Ibnul Hanafiyyah) da kuma Umar da Abbas.

Wannan matsayi kuwa na Rafilawa, ko a littafansu akwai ruwayoyin da su ka ci karo da shi kamar ruwayar da al-Arbili (daga cikin manyan malamansu) ya ruwaito a cikin littafin Kashful Gummati,[16] cewa an tambayi Manzon Allah (SAW) cewa; su wane ne Iyalan gidansa? Sai ya amsa da cewa, su ne iyalan gidan Ali da na Ja'afar da na Aƙilu da na Abbas.

A nan gaba mai karatu zai gamu da cikakken bayani game da matsayin Rafilawa ('yan Shi'ah) akan **Ahlulbaiti** a Babi mai zaman kansa. Amma mun zo da wannan bayanin ne a nan domin mu kwatanta tsakanin matsayar Ahlus Sunnah da ta 'yan Shi'ah, sai mai karatu ya yi hukunci da kansa.

16 Duba: Kashful Gummati na al Arbili, 1/43.

# BABI NA BIYU

## 2.0 Martabobin Ahlulbaiti

Wannan babi zai kalli irin martabobin da jinsunan mutanen da muka yi bayani a baya ke da su, a matsayinsu na **Ahlulbaiti** daga maɓuɓɓugar musulunci ta asali (alƘur'ani da Sunna). Haka babin zai taɓo bayani a kan irin haƙƙoƙan da, waɗannan mutane ke da su a kan musulmi a mahanga ta Ahlus-Sunnah.

## 2.1 Darajojinsu a cikin Alƙur'ani

Allah Maɗaukakin Sarki na cewa, a cikin Al-ƙur'ani:-

﴿ إِنَّمَا يُرِيدُ اللَّهُ لِيُذْهِبَ عَنْكُمُ الرِّجْسَ أَهْلَ الْبَيْتِ وَيُطَهِّرَكُمْ تَطْهِيرًا﴾

(الأحزاب:٣٣)

**(Allah na nufin ne kawai ya tafiyar da ƙazanta daga gare ku, ya Ahlulbaiti**

(Mutanen Babban Gida!) kuma ya tsarkake ku tsarkakewa.

[Suratur Ahzab : 33]

A cikin wannan aya, Allah ya fito da martabar waɗannan mutane, ta bayyana nufin Ubangiji na tsarkake su daga duk wata ƙazanta, wadda ta haɗa da; Shirka da miyagun ɗabi'u, irin na Allah waddai, kamar; rowa da Hassada da Sauransu.

Haka kuma yana cewa:

﴿ إِنَّ اللَّهَ وَمَلَائِكَتَهُ يُصَلُّونَ عَلَى النَّبِيِّ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا صَلُّوا عَلَيْهِ وَسَلِّمُوا تَسْلِيمًا ﴾

(الأحزاب:٥٦).

"Lalle Allah da Mala'ikkunsa su na salati ga

Annabi. Ya ku waɗanda suka yi Imani! ku yi Salati a gare shi, kuma ku yi sallama domin amintarwa a gare shi"

[Suratul Ahzab : 56]

Ka'abu ɗan Ujrata (RA) yace: "Mun tambayi Manzon Allah (SAW), a lokacin da wannan aya ta sabka, cewa: mun dai san yadda ake sallama gare ka, ya Manzon Allah, to ya za mu yi maka salati? Sai ya ce; "ku ce Allah ka daɗa tsira bisa ga Iyalan Muhammadu". Ko shakka babu wannan babban martaba ce.[17]

Alƙur'ani ya darajanta Matan Manzon Allah (SAW) matuƙa, ya kira su iyayen Mummunai, ya haramta aurensu bayan Manzon Allah, kuma ya bayyana cewa,

---

[17] Sahih al Bukhari, Kitabul Tafsir, Hadisi na 4797.

darajarsu ta zarce ta dukkan mata. Mu duba waɗannan ayoyi:

﴿يَا نِسَاءَ النَّبِيِّ لَسْتُنَّ كَأَحَدٍ مِنَ النِّسَاءِ إِنِ اتَّقَيْتُنَّ فَلَا تَخْضَعْنَ بِالْقَوْلِ فَيَطْمَعَ الَّذِي فِي قَلْبِهِ مَرَضٌ وَقُلْنَ قَوْلًا مَعْرُوفًا (٣٢)﴾

[الأحزاب].

**Ya matan annabi! Ba ku zama kamar kowa ba daga mata, idan kun yi taƙawa, saboda haka kada ku sassautar da magana har wanda ke da cuta a cikin zuciyarsa ya yi ɗammani, kuma ku faɗi magana ta alheri.**

﴿وَمَا كَانَ لَكُمْ أَنْ تُؤْذُوا رَسُولَ اللَّهِ وَلَا أَنْ
تَنْكِحُوا أَزْوَاجَهُ مِنْ بَعْدِهِ أَبَدًا إِنَّ ذَلِكُمْ كَانَ
عِنْدَ اللَّهِ عَظِيمًا (٥٣)﴾ [الأحزاب]

Kuma bai kamata a gare ku ba ku muzguna ma Manzon Allah, haka (bai halalta) a gare ku ba ku auri matansa a bayansa har abada. Lalle wannan ya kasance (laifi ne) babba a wurin Allah. Suratul Ahzab: 53

﴿النَّبِيُّ أَوْلَى بِالْمُؤْمِنِينَ مِنْ أَنْفُسِهِمْ وَأَزْوَاجُهُ
أُمَّهَاتُهُمْ(٥)﴾[الأحزاب]

Annabi shi ne mafi cancanta da

**mummunai daga kawunansu. Kuma matansa iyayensu ne. Suratul Ahzab: 5**

Zuri'ar Manzon Allah su ma su na da wata daraja a alƙur'ani, ita ce, saukar da su da Allah (SWT) zai yi masaukin Manzonsa saboda kusancinsu na dangantaka da shi. Ga wannan bayanin a cikin:

﴿ وَالَّذِينَ آمَنُوا وَاتَّبَعَتْهُمْ
ذُرِّيَّتُهُمْ بِإِيمَانٍ أَلْحَقْنَا بِهِمْ
ذُرِّيَّتَهُمْ وَمَا أَلَتْنَاهُمْ
مِنْ عَمَلِهِمْ مِنْ شَيْءٍ كُلُّ
امْرِئٍ بِمَا كَسَبَ رَهِينٌ
(٢١)﴾ [سورة الطور].

**"kuma waɗanda suka yi Imani, kuma Zuriyarsu su**

ka bi su ga imanin, mu na riskar da zuri'arsu da su, ba da mun rage musu kome ba daga aikinsu, kowane mutum jingina ne ga abinda ya sana'anta"

[Suratul Ahzabi: 21]

Idan mu na son mu taƙaice, mu na iya cewa, duk inda Allah (SWT) ya yabi sahabbai, a cikin Al-Kur'ani, to Iyalan Annabi (SAW) su na cikinsa. Wannan ko ya wuce a ƙirga shi.

Abin da muka kawo anan mun kawo shi ne a dunƙule dangane da darajojin da su kayi tarayya akan su. Darajojin ɗaiɗaikunsu na nan a shimfiɗe cikin littafai. Wasu kuma sun gabata dangane da Matan Manzon Allah (SAW). Amma don neman ƙarin bayani mai karatu na iya komawa ga mafi ingancin littafai waɗanda aka tace su daga duk ruwayoyi marasa tushe da masu rauni,

Sahihul Bukhari da Sahihu Muslim, ko wannensu ya ware Babi mai zaman kansa akan darajojin ɗaiɗaikun **Ahlulbaiti** da Sahabbai.

## 2.2 Darajojinsu a cikin Hadisi (Sunnah)

Akwai Hadisai da dama, da suka yi magana a kan martabobi da darajojin **Ahlulbaiti.** Za mu taƙaita bincikenmu a kan wasu Hadissai ingantattu guda bakwai (7). Amma bari mu soma da waɗannan guda biyu waɗanda su ke bayyana fifikon dangin nasa baki ɗaya akan sauran mutane:

1. Tirmizi ya ruwaito, a cikin Babin falalar Annabi (SAW) Cewa: Abbas (R.A) ya ce : "Na ce wa Manzon Allah (SAW): Kuraishawa sun zauna suna bitar tarihin gidansu. Sai suka kwatanta ka da mariccin kan dutse. Sai Annabi (SAW) ya ce:

> "Da Allah ya tashi samar da halitta, sai ya zaɓi mafi alherinta ya sanyo ni a ciki. Ya kuma zaɓi mafi alherin ƙabilu ya sanyo ni a ciki. Ya kuma zaɓi mafi alherin gidaje ya sanyo ni a ciki. Saboda haka ni

> ne mafi alherinsu ga tushe da asali”.

Hadisi na biyu da ya daɗa fitowa da manufar a fili, shi ne:

2. Muslimu ya ruwaito daga Wasilatu ɗan Asƙa’u wanda ya ce: “Na ji Manzon Allah (SAW) na cewa:

> “Haƙiƙa Allah ya zaɓi kinanata daga cikin ‘ya’yan Isma’il. Daga cikin Kuraishawa kuma ya zaɓi Banu Hashim. Daga cikin Banu Hashim kuma ya zaɓe ni”.

Mu na iya lura daga waɗannan hadissai guda biyu cewa, Manzon Allah (SAW) an zaɓo shi ne daga dangi zaɓaɓɓu. Don haka, duk wanda ya ke tunanin ya san darajar Manzon Allah (SAW) amma bai san darajar danginsa ba, to bai gano asalin Manzon Allah ɗin ba kenan.

Haka kuma za mu lura cewa, Manzon Allah (SAW) ya na kula da zumunsa na kusa da na nesa, ya na yi mu su addu’a, kuma ya na yi wa musulmi wasicci da su ƙaunace su, su kula ma sa da su, su kyautata a gare su a

matsayin wani haƙƙinsa a kan musulmi. Mu duba wannan hadisi:

3. Hakimu ya ruwaito, a cikin "Al-mustadrak", Imam Zahabi ya ingantantar da ruwayar daga Hadisin ɗan Abbas (R.A) cewa, Manzon Allah (SAW) ya ce:

> "Ya ku Bani Abdil Muɗɗalib[18], ku sani na roƙar maku Allah, abubuwa guda Uku:
>
> 1- Allah ya tabbatar da duga dugan waɗanda ke tsaye daga cikinku.
> 2- Ya kuma shiryar da wanda ya yi ɓatan kai daga cikinku.
> 3- Ya kuma sanar da jahilanku.
>
> Na kuma roƙe shi ya sanya ku masu tsananin alheri, da juriya da jinƙayi.
>
> Kuma lallai da wani mutum zai yi Sallah, tsakanin Rukuni (Hajarul Aswad) da Al

[18] Banu Abdil Muɗɗalib su ne, waɗannan da muka lisafto, 'yan uwan haifuwar mahaifinsa da zuri'arsu.

Maƙam (Maƙamu Ibrahim)[19], yana kuma ɗauke da azumi, idan ya mutu ya na ƙin iyalan Muhammadu, to makomarsa ita ce wuta.[20]

Game da dangi na kusa kenan. To, game da na nesa kuma, mu karanta wannan hadisi:

4. Muslim ya ruwaito daga Abu Zar (RA) ya ce; Manzon Allah (SAW) ya ce:

Lalle ne za ku ci ƙasar da ake kira Misra, sunan kuɗinsu Kirat. Idan ku ka ci garin to, ku kyautata ma mutanensa, domin su na da alƙawali (akanku) da zumunta. Ko kuma yace, alƙawali da surukuta.[21]

Imam an Nawawi ya fayyace mana wannan wasiyya a in da ya ke cewa,

---

[19] Wannan hadisi ya nuna darajar wannan wurin daga jikin ka'aba, da muhimmancin yin ibada a cikinsa.

[20] Al Mustadrak, na Hakim, Kitabu "Ma'arifatis Sahabah", Babin darajojin Iyalan Annabi (SAW) (3/149-148).

[21] Sahihu Muslim, Kitabu Fadail ashabin Nabiy, Hadisi na 2543.

Malamai sun ce: Zumuntar misrawa ita ce, auren da kakan Manzon Allah (SAW), Annabi Ibrahimu (AS) ya yi da ‘yar garinsu, Hajar. Surukuta kuwa ita ce, kasancewar uwar Ibrahim ɗan autan Manzon Allah (SAW) bamisriya ce.[22]

Sai mu je zuwa ga wasiccin Manzon Allah (SAW) game da danginsa mafi kusanci, su ne; **Ahlulbaiti**:

5. A cikin Sahihu Muslim, Zaidu ɗan Arƙamu ya ruwaito cewa, Manzon Allah (SAW) ya ce a cikin wata huɗuba da ya yi a dai dai wani tafki da ake kira “Gadir Khum”:

> “Bayan haka, ku sani ya ku mutane, haƙiƙa ni mutum ne da Manzon Ubangijina ya kusa ya zo mi ni in karɓa masa (Yana nufin mutuwa). Zan bar amanar wasu abubuwa guda biyu, a hannunku. Na farko shi ne; Littafin Allah, a cikinsa akwai shiriya da haske; ku yi riƙo da Littafin Allah, riƙo na

[22] Duba: Riyadus Salihin, na Nawawi, tare da sharhinsa mai suna Nuzhatul Muttaƙin (1/368).

sosai. Ya yi matuƙar jan hankalin mutane zuwa ga Littafin Allah. Sannan ya ce: Da kuma Iyalan Gidana, ku riƙe su matsayin amanar Allah, ku riƙe su matsayin amanar Allah..”[23]

Wannan hadisin ya shahara da sunan hadisin Gadir. Kuma ingantacce ne a wurin kaffatanin malaman Sunnah. Ya na kuma ɗaya daga cikin hujjojin Ahlul Sunnah na darajanta Iyalan Manzon Allah (SAW). Amma a wurin Rafilawa (‘yan Shi’ah) sai su ka faɗaɗa hadisin, su ka ce, ai Annabi (SAW) bai tsaya nan ba ma sai da ya sa aka yi mubaya’a ga Sayyiduna Aliyu a matsayin mai gadonsa. Daga nan su ka soma kushe wa Sahabban Manzon Allah (SAW) saboda ba su ga an zartar da wannan mubaya’ar ba a bayan cikawarsa. To, ina laifin sahabbai in

[23] Wasu malamai na ganin cewa, daga wannan hadisin Manzon Allah (SAW) ya nisantar da iyalan gidansa daga harkar mulki. Domin kuwa, da ace su ne ya ke nufin su jagoranci sha’anin al’ummarsa, da su zai yi wa wasicci da su riƙe amana, ba su zai ce a riƙe ba.

ya kasance su ba su san da wannan mubaya'a da 'yan shi'ah su ka kitsaa cikin ƙwaƙwalwarsu ba, su dai sun yi aiki da abin da su ka sani a alƙur'ani da hadisi cewa, al'amurran musulmi shawara ne a tsakaninsu? Sun kuma yi shawara sun tsai da wanda su ke ganin ya fi cancanta. Da shiga ta zo ga Aliyyun kuma sun zaɓe shi. Mu je ga sauran hadissai biyu da su ka rage mana akan falalar **Ahlulbaiti** da haɗarin yin adawa da su:

6. A cikin Sahihu Muslim har wayau, hadisi ya zo a cikin Babin Falalar annabi (SAW), daga Safiyyatu 'yar shaibatu, ta ce, A'ishah (R.A) ta ce: Wata rana Annabi (SAW) ya fita da hantsi, ya na sanye da wani baƙin mayafi mai kauri, sai ga Hassan ɗan Aliyu, sai ya sa shi cikin mayafin. Sai kuma ga Hussaini, shi ma ya saka shi. Sai kuma ga Faɗimatu, ita ma ya saka ta, sai kuma ga Ali (R.A) shi ma ya saka shi. Sannan ya karanta ayar da ta ce:

﴿ إِنَّمَا يُرِيدُ اللَّهُ لِيُذْهِبَ
عَنْكُمُ الرِّجْسَ أَهْلَ الْبَيْتِ

وَيُطَهِّرَكُمْ تَطْهِيرًا﴾

(الأحزاب:٣٣)

**(Allah na nufin ne kawai ya tafiyar da ƙazanta daga gare ku, ya Ahlulbaiti (Mutanen Babban Gida!) kuma ya tsarkake ku tsarkakewa.**

**[Suratur Ahzab : 33]**[24]

7. Hakimu kuma ya ruwaito hadisi daga Abu Sa'id (R.A) cewa, Manzon Allah (SAW) ya ce:

"Na rantse da wanda rayuwata ke hannunsa, duk wanda ke ƙiyayya da ɗaya daga cikinmu;

[24] Sahihu Muslim, Hadisi na 2424.

**Ahlulbaiti (**‘yan gidan annabta), wuta Allah zai sa shi.[25]

## 2.3 Haƙƙoƙin Ahlulbaiti a kan Musulmi

Iyalin gidan Manzon Allah (SAW) na da waɗansu haƙƙoƙa guda Uku (3), waɗanda suka wajaba a kan kowane Musulmi. Ga su kamar haka:

(a) Kauna da Girmamawa: Iyalin gidan Manzo na da, wani matsayi a cikin al’umma, da ke wajabta ƙaunarsu da girmama su, fiye da kowa. Abubuwan da muka ambata a baya ma, sun isa hujja a kan wannan. Ba sai mun nemi kafa wata sabuwar hujja ba.

(b) Yi ma su salati tare da mai gidansu: Yi wa **Ahlulbaiti** Salati tare da Manzon Allah (SAW) na daga cikin haƙƙoƙansu a kan Musulmi mai bin tafarkin Sunnah. Don Allah (SWT) ya ce:

---

[25] Al Mustadrak, na Hakim, Kitabu “Ma’arifatis Sahabah, Babin darajojin Iyalan Annabi (SAW)” (3/150).

﴿ إِنَّ اللَّهَ وَمَلَائِكَتَهُ يُصَلُّونَ عَلَى النَّبِيِّ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا صَلُّوا عَلَيْهِ وَسَلِّمُوا تَسْلِيمًا ﴾ (الأحزاب:٥٦).

**"Lalle, Allah da Mala'ikunsa suna Salati ga Annabi. Ya ku waɗanda suka yi imani ku yi Salati a gare shi, kuma ku yi Sallama domin amintarwa a gare shi".**

Kuma shi Manzon Allah (SAW) da ya bayyana wa Sahabbai yadda wannan Salati zai kasance, ya gaya ma su, su shigar da iyalansa. Mun kawo wannan hadisin a can baya,

(c) Biyayya : Biyayya da koyi da managarta, daga cikin Iyalan Manzon Allah (SAW) shi ma wajibi ne, a kan duk wanda ke koyi da Manzon Allah (SAW).

# BABI NA UKKU
## 3.0 Alaƙar magabata da Ahlulbaiti

Wannan babi, zai kalli irin kyakkyawar alaƙa da zumuncin da ya wanzu, tsakanin magabatan wannan al'umma, da suka haɗa da wasu Sahabbai, musamman Sayyiduna Umar (R.A) da kuma dangin Banu Umayya waɗanda 'yan shi'a ke fafutukar gamsar da mu cewa, su ne maƙiyan **Ahlulbaiti.**

### 3.1 Matsayin Ahlulbaiti a wurin halifofi:

**Ahlulbaiti** na da babban matsayi a wurin magabata; kamar yadda magabatan ke da shi a wurinsu. Tarihi ya nuna cewa, akwai matuƙar soyayya da ƙauna da girmama juna a tsakanin waɗannan manyan mutane, wa-su wa-su, da kuma tsakanin ɓangaroran biyu. Kamar yadda Allah (SWT) ya siffanta su ga baki ɗaya da cewa :

﴿ أَشِدَّاءُ عَلَى الْكُفَّارِ رُحَمَاءُ بَيْنَهُمْ (٢٩)﴾ [الفتح].

**"…masu tsanani**
**ne a kan kafirrai,**
**masu rahama ne a**

tsakaninsu”
[Suratul Fathi :
29].

### 3.1.1 Matsayin Khalifa Abubakar (RA):

Bukhari ya ruwaito daga Sayyiduna Abubakar (R.A), ya ce : “ku girmama Iyalan gidan Muhammadu (SAW) saboda shi”.[26]

Ya kuma ce wa Sayyiduna Ali (R.A): Na rantse da wanda rayuwata ta ke hannunsa, dangin Manzon Allah (SAW) da Iyalansa, sun fi soyuwa gare ni, bisa ga dangina da iyalaina.”[27]

### 3.1.2 Matsayin Khalifa Umar (RA):

Daga ruwayoyi na tarihi da su ke a gabanmu, na shi’ah da na Sunnah, mu na iya cewa, ba wani khalifan da ya bayyana ma iyalan Manzon Allah (SAW) ƙauna kamar Sayyiduna Umar. Ya kasance ya na mutunta su manyansu da ƙananansu. Daga cikin ƙaunar da ya ke nunawa ga ‘yan tagwayen[28]

---

[26] Sahihul Bukhari, Hadisi na 713.

[27] Sahihul Bukhari, Hadisi na 3712 da Sahihu Muslim, Hadisi na 1759

[28] Hassan da Hussaini ba tagwaye ba ne. An haife su ɗaya bayan ɗaya da tazarar shekara ɗaya kawai a

Manzon Allah (SAW) ne ya zaɓar ma Hussaini ‘yar Sarkin Farisa mai suna Shaharbanu, a lokacin da mutane na zaton cewa, zai zaɓa ma kansa ita, ko ya ba ɗansa, bisa ga abin da aka saba a tsarin sarakuna (‘yar sarki ta auri sarki ko ɗansa). Shaharbanu ta kasance mai tsananin kyawo wanda ya ɗauki hankalin kowa a lokacin da aka zo ma Sayyiduna Umar da ita. Hussaini kuwa ya yi murna da wannan kyauta, domin kuwa ita kaɗai ya zauna da ita, har ta Haifa masa duk ‘ya’yansa, daga cikinsu har da Sukainah wacce aka ce, ba’a taɓa yin balaraba kyakkyawa ba irinta.

Akwai wani labari da Ibnu Abil-Hadid (daga cikin malaman Shi’ah) ya kawo, a Sharhinsa na Nahjul-Balaga[29] wanda ke nuna mana irin girman da **Ahlulbaiti** ke da shi, musamman ‘yan

---

tsakaninsu. Amma mu hausawa mun saba da ɗaukarsu a matsayin tagwaye, har ma duk inda mu ka samu tagwaye, mu kan sa mu su wannan suna. To, da yake kusancinsu ya na kama da na tagwaye, kuma ga al’adar Malam Bahaushe ta kiransu da wannan suna, sai muka tafi a hakan. Mu lura da wannan.

[29] Sharhin Nahjul-Balaga (3/110).

tagwayen Manzon Allah (SAW) a wurin Umar (RA). Ga abin da ruwayar ta ke cewa:

Wata rana Umar ya aika ya na neman Sayyiduna Hussaini don wata buƙata. Da Hussaini ya kama hanyarsa, sai ya ci karo da Abdullahi ɗan Umar. Hussaini ya gaya masa cewa, zai je karɓa kiran babanka ne. Sai Abdullahi ya ce ma sa: "Ai ko yana da wuya ka sami ganinsa; don ni ma na so haka, abin ya faskara, don bai yi ma ni izni ba". Jin haka sai Husani ya koma. Da ya dawo a kashegari ya sadu da Umar, Umar ya tambaye shi dalilin da ya sa bai ganshi ba a jiya, sai ya ba shi labarin yadda suka yi da Abdullahi. Sai Umar ya ce masa: "To hala matsayinku ɗaya da shi a wurina? Ko ka taɓa jin akwai wani mai girma da ɗaukaka a wurina irinku; Iyalin Babban Gida?".

Wata rana kuma Umar ya aike ma 'yar uwarsa As Shifa'u bint Abdillah domin tazo yana son ganinta, ko da tazo sai ta tarar da wata baƙuwa wadda ita ce Atika bint Usaid, a lokacin da Umar ya gansu a tare sai ya ɗauko wasu mayafai guda biyu babba da ƙarami, ya bai wa Atika babbar ita kuma Shifa'u ya ba ta ƙarami. 'Yar uwarsa ba ta

ɓoye damuwarta ba akan wannan banbanci sai tace masa, haba Sarkin Musulmi, kai ne fa ka aika kira na wannan kuma ita tazo da kanta, a musulunta kuma na riga ta, sannan ni 'yar uwarka ce, ya za kayi min haka? Umar ya amsa mata da cewa, a haƙiƙa na kira ki ne don in baki su duka, amma da na ganta na tuna kusancinta da Manzon Allah (SAW) sai naga ta fi dacewa da in ba ta babba,don haka sai ki yi haƙuri.[30]

Bari mu koma ta wani ɓangare don mu ga irin matsayi na gatanci da **Ahlulbaiti** ke da shi a gwamnatin Umar. A lokacin khalifa Umar ɗan khaɗɗabi ne (R.A) a ka yawaita jihadin faɗaɗa biranen musulunci. A sakamakon haka kuwa dukiya ta yawaita ainun a cikin taskar musulmi, saboda ganima da fai'i da haraji da jangali da makamantansu. Don haka Sayyiduna Umar ya yanke shawarar kafa Ma'aikatar kula da jin daɗin jama'a, wadda za ta yanka albashi ga talakawan daularsa baki ɗaya.

Mataki na farko da Sayyiduna Umar ya ɗauka shi ne, na kafa kwamiti don

[30] *Al Isabah* na Ibnu Hajar, (4/25).

fayyace yawan jama'a da yi ma su rajista bisa ga cancantarsu. Ya kafa wannan kwamitin ne a ƙarƙashin jagorancin Aƙilu ɗan Abu ɗalib, shaƙiƙin sayyiduna Ali. Sauran membobinsa kuma sun haɗa da, Makhramatu ɗan Naufal da Jabiru ɗan Muɗ'imu ɗan Naufal ɗan Abdu Manaf. Ya kuma umarce su da cewa : "ku tsara sunayen mutanen da za su ci gajiyar wannan shiri, gwargwadon matsayinsu daga Manzon Allah (SAW)".

Rahoton farko na wannan kwamiti ya tsara mutane bisa ga kusancinsu da Manzon Allah (SAW) amma ba yadda Umar ya ke so ba. Domin su, sun yi la'akari da kusanci na zamantakewa ne da ƙauna, shi kuma ya na umurninsu ne da su tsara bisa ga kusanci na zumunta. Don haka, a maimakon farawar da su ka yi da Iyalin Abubakar sannan Umar, ya umurce su da rubuta Ali da Abbas da sauran dangin Manzon Allah (SAW) kafin sunansa shi kansa. Har ma da ya ga sunansa a in da su ka ajiye shi, sai ya ce, "Wallahi na so a ce ma kusancina da Manzon Allah ya kai haka, amma ku fara da Manzon Allah (SAW), sannan danginsa daki-daki, ku aje

Umar inda Allah ya aje shi". A ka fara rubuta Banu Hashim, sannan Banu Abdil Muɗɗalibi, sannan Banu Abdi Shamsi da Naufalu. Haka dai aka biyo ta kan ƙuraishawa daidai kusancinsu, sannan aka zo ga sauran mutane. Wannan rajista ta Sayyiduna Umar kuwa ta daɗe tana aiki har a zamanin daulolin da su ka biyo baya.

A bisa ga wannan rajista kuwa, Sayyiduna Ali shi ne ya fi kowa samun kaso mai tsoka, in ban da Matan annabi (SAW) da ɗan uwan babansa Abbas. Sai ga khalifan da kansa ya na karɓar albashi ƙasa da na iyalan Manzon Allah (SAW).

Haka kuma a cikin bitar da Umar ya ke yi wa rajistar, ya tarar da sunayen Hassan da Hussaini a matsayinsu na 'ya'yan Ali dai dai da sauran ƙananan yara 'ya'yan Sahabbai, su na da Dirhami dubu biyu ko wanensu. Amma sai Sayyiduna Umar ya cire su, ya riskar da su da babansu, aka yanka masu dubu biyar-biyar, yace, saboda

kusancinsu da Manzon Allah da irin son da Manzon Allah (SAW) ɗin yake yi masu.[31]

Abdullahi ɗan Umar ya yi koke game da nasa albashin, domin Sayyiduna Umar ya ƙara ma Usamatu ɗan Zaidu Dirhami ɗari biyar a kan albashinsa. Shi kuma a ganinsa, ba wani abin da ya raba shi da Usama, domin su tsara ne, waɗanda su ka tashi tare, su ka je wuraren jihadi ɗaya tare da Manzon Allah (SAW). Amsar da Babansa ya ba shi ita ce: "Na fifita shi ne a kanka, don Manzon Allah ya fi sonsa akanka, ya kuma fi son mahaifinsa akan naka"[32]

A cikin mata nannabi (SAW) ma, sai da Umar ya fifita Nana A'ishah akan sauran mata (waɗanda su ka haɗa da ɗiyarsa Hafsah), la'akari da fifikonta wajen son da Manzon Allah (SAW) ya ke yi mata. Duk da ya ke wasu ruwayoyi sun bayyana cewa, ita A'ishar ta yi masa magana akan cewa, tun da Annabi (SAW) bai banbanta su ba a

[31] Duba: al Tarikh, na Ya'aƙubi, (2/153) al Ɗabaƙat, na Ibnu Sa'ad (3/213-214) da Al Kharaj, na Abu Yusuf, Shafi na 43-44.

[32] Minhajus Sunnatin Nabawiyyah (3/172-173).

kyautukansa, shi ma ya daidaita su. Sa’annan ya mayar da albashinsu iri ɗaya.

Idan mu ka koma wajen sauran dangin Annabi (SAW), za mu ga irin matsayin da su ke samu a wurinsa. Misali, Umar ne kaɗai a zamanin mulkinsa ya ke kusanto da ƙanin Manzon Allah (SAW), Abdullahi ɗan Abbas, duk da ƙanƙantarsa. Idan aka yi masa magana ya kan ce: “Yaro da gari abokin tafiyar manya ne”. Ya na nuni da irin ilmin da ya ke da shi.

Game da mahaifin nasa kuma (Ina nufin Abbas, baffan Manzon Allah (SAW), Umar ya taɓa yin ciris da fushinsa. Wannan ya faru a lokacin da aka buɗa garin Makkah, domin shi Umar ɗin ya na da ra’ayin duk a gama da maƙiyan musulunci waɗanda suka ƙare rayuwarsu wajen yaƙar Manzon Allah (SAW). Shi kuma Abbas ya na da ra’ayin a yafe masu. Da zancen ya haɗa su sai Abbas ya fusata, ya ce, don dai ba su na ‘yan ƙabilarka ba ne! Anan sai Umar yace masa, Ni, ba ni da wani ƙabilanci ga jama’ata akan musulunci. Don wallahi ranar da ka musulunta na fi farin ciki bisa ga a ce khaɗɗabi ne, babana, ya musulunta, don

kuwa na san irin farin cikin Manzon Allah (SAW) a kan musuluntarka.

### 3.1.3 Matsayin Sayyiduna Usman (RA):

Shi kuwa Sayyiduna Usman (RA) shi ya ɗauki nauyin hidimar auren Sayyiduna Ali (RA) da Fatimatu, wanda ya lashe dirhami dubu huɗu (4000) bisa ga ruwayar da ta ke a cikin littafan Shi'ah. Sun kuma bayyana cewa, Abubakar ne da Umar (RA) su ka ba shi shawarar neman auren tun da farko.[33]

Game da Hassan da Hussaini, sun kasance su na samun matuƙar karramawa da khalifa Usman, har ma ya kan shugabantar da su a wurin jihadi. Bai kuma taɓa fifita wani a kansu ba, ga rabon ganima, ko waye shi. A sakamakon wannan ƙauna ne, da Usman ke yi wa Hassan da Hussaini, su kuma suka taimake shi, ranar da aka kai masa hari a gidansa. Wasu ruwayoyi sun bayyana cewa ma, mahaifinsu Ali (RA) ne ya ba su umarnin kare shi.

---

[33] *Kashful Gummah*, na Arbali, (1/358 – 359) da *Biharul Anwar*, na Majlisi, 39 – 40 da *Al Manaƙib*, na Khuwarizami, (251 – 253).

Ya kuma zo a cikin littafin: Tarikhul Umam Wal Muluk, cewa, a lokacin da aka kai wa Sayyiduna Usman hari, ya shugabantar da ɗan Abbas akan aikin hajji. Abbas ya ce masa, shi ya fi son a bar shi ya kare Sarkin Musulmi, sai da Sayyiduna Usman ya tsaya kai da fata a kan shi ɗan Abbas ya wakilce shi, sannan ya tafi.[34]

### 3.1.4 Matsayin Ali (RA) a game da sauran halifofi

Sayyiduna Ali (R.A) na ɗaya daga cikin waɗanda Umar (RA) ya ke kusantar da su, ya na neman shawararsu a matsayin 'yan majalisar zartaswa na gwamnatinsa, har ma ya kan nemi Allah tsari da faruwar matsala a lokacin da Ali ba ya kusa.

A lokacin halartowar ajalinsa kuwa, Ali na daga cikin waɗanda ya zaɓa, don a tsayar da khalifa daga cikinsu, a kan hujjar cewa, dukkansu Manzon Allah (SAW) ya yarda da su.

---

[34] Duba: *Tarikhul Umam Wal Muluk*, na Tabari, a abubuwan da su ka faru a shekara ta 35B.H. da *Murujuz Zahab*, na Mas'udi, (2/344).

Tarihi ya tabbatar da cewa, akwai mutunci a tsakanin Umar da Ali (R.A) har shi Ali ya ce a ranar da aka soki Umar, kafin cikawarsa: "Ba wani mahaluki a bayan ƙasa da ya rage wanda nake fatar in haɗu da Allah da irin aikinsa bayan Umar. Kuma wallahi na kyautata zaton za ka haɗu da Manzon Allah da Abubakar wuri ɗaya gobe ƙiyama, da yardar Allah. Don da yawa ni kan ji Annabi (SAW) na cewa: mun tafi wuri kaza tare da Abubakar da Umar, mun shiga wuri kaza tare da Abubakar da Umar, mun fita daga wuri kaza tare da Abubakar da Umar.[35]

Wata rana kuma, a cikin kwanukkan ƙarshe na Ali (R.A) an tambaye shi cewa : me zai hana ya zaɓi wanda zai gade shi. Sai ya karɓa da cewa: in da Manzon Allah ya yi haka, da na yi. Amma idan Allah ya yi nufin alheri gare ku, to zai haɗa hankalinku a kan mafi alherinku, kamar yadda ya haɗa hankulan Sahabbai bayan Annabi, a kan mafi alheri daga cikinsu.

---

[35] Wannan labarin dukkan maruwaitansa daga **Ahlulbaiti** ne. Duba shi a cikin Sahihul Bukhari.

Kuma Sayyiduna Ali (R.A) shi ya ke cewa: "Mun yarda da shugabancin wanda manzon Allah ya shugabantar mana a cikin sha'anin addininmu ya shugabancemu a cikin sha'anin duniyarmu".[36]

Shi kuma ya ce : "mafi girman daraja a cikin wannan al'umma bayan Manzon Allah, su ne Abubakar da Umar (R.A).[37]

---

[36] Ya na nuni ga cewa, tun da Manzon Allah (SAW) ya shugabantar da Abubakar ga sallah, mu mun amince da ya shugabance mu a siyasa.

[37] Duk waɗannan kalamai na gaskiyar Allah da sayyiduna Ali ya furta don bayyana gamsuwarsa da halifofin da su ka gabace shi, a wurin 'yan shi'a taƙiyyah ce (kissa) ya ke yi wai don a zauna lafiya. Ma'ana dai a wurinsu shi matsoraci ne, wanda Allah ya ba shi haƙƙe, Annabi ya tabbatar ma sa, amma kuma aka ƙwace ma sa ya na ji ya na gani, bai iya yin komai, sai 'yan muzurrai ya ke, ya na neman kare kansa don kar a ɗauke shi ɗan tawaye a halaka shi. Alhalin kuwa in ka fara jin 'yan shi'a – na da ko na yanzu – su na wasa shi da jaruntaka da taron ko wace irin aradu kai ka ce ko sarkin aljannu ya ƙwaci haƙƙinsa ba zai sha da daɗi ba. Abin da ya kamata mu yarda da shi shi ne cewa, abin da duk ya faɗa tsakani da Allah ya faɗe shi ba munafurci, kuma wannan abin da ya kamace shi kenan.

## 3.2 Matsayin Ahlulbaiti a wurin Ahlus Sunnah baki ɗaya

Son **Ahlulbaiti** da mutunta matsayinsu bai taƙaita ga khalifofi ba kawai ko Sahabbai, a'a duk musulmi na kirki, mai bin Sunnah, ya na da wannan matsayi a game da su. A nan za mu ba da 'yan misalai ne kaɗan daga tarihi sauran magabata a bayan Sahabbai don tabbatar da gaskiyar wannan magana da mu ka yi:

### 3.2.1 Matsayin Umar ɗan Abdul Aziz:

Wata rana Abdullahi ɗan Al-Hassan ɗan Hassan ɗan Aliyu, ya zo wurin Sarkin Musulmi Umar ɗan Abdul Aziz ya na neman wata buƙata. To, bayan da ya biya masa da buƙatar, sai kuma Umar ya ce masa: "Daga yau idan kana da wata buƙata, ba sai ka taho ba, ka aiko kawai, ta baki, kana nemana, ko ka rubuto min buƙatarka. Don ni, ina jin kunyar Allah, ya ga jikan Manzonsa ya na doddofa a ƙofar gidana.[38]

Kuma Umar ɗan Abdul-Aziz ya taɓa ce wa Faɗimatu 'yar Ali ɗan Abu ɗalib: Ya ke 'yar Ali, ki sani, ina rantsuwa da Allah, a

---

[38] Asshifa, na Alƙali Iyad, (2/49-50).

yau babu wasu iyalan gida a bayan ƙasa da nake so, kamarku. Wallahi zuri'arku ita ce mafi soyuwa gare ni a kan zuri'ata".

### 3.2.2 Matsayin Imamu Malik

Wata rana, Ja'afaru ɗan sulaimanu, a lokacin da yake gwanna a madina, ya sa aka yi wa Imamu Malik bulala akan wata fatawa da ya yi, wadda gwamnan ke ganinta a matsayin zuga ce ga talakkawa akan su yi bore. To, a bayan haka ne aka tambaye shi, game da wannan abin da ya faru, sai ya ce, ai na yafe masa, domin ina jin kunyar haɗuwa da Manzon Allah, idan na yi sanadiyyar, ɗaya daga cikin Zuri'arsa ya shiga wuta".[39]

### 3.2.3 Matsayin Imamu Ahmad

Haka Imamu Ahmad ɗan Hambali, a duk lokacin da wani daga cikin Banu Hashim ya je karatu wurinsa a masallaci, ya kan taso ya raka shi, don girmamawa; yana gaba baƙon na biye, har ya yi sallama da shi

[39] Asshifa, na Alƙali Iyad, (2/51).

idan sun fito masallaci. Ba ya yi wa kowa haka in ba dangin Annabi ba.[40]

## 3.3 Wasu alamomi na kyakkyawar alaƙa a tsakanin Ahlulbaiti da sauran Sahabbai

Akwai wasu abubuwa da dama da yin nazari akansu zai taimaka muna ainun wajen gano irin kyakkyawar dangantaka da alaƙar da ta wanzu a tsakanin waɗannan bayin Allah. Za mu kawo wasu daga cikinsu.

### 3.3.1 Ahlulbaiti su na koyi da Sahabbai

Mun riga mun gabatar da maganar Sayyiduna Ali (RA) game da yabon Sayyiduna Umar, da fatar da ya ke yi na ya haɗu da Allah da irin aikinsa.

Haka ma sauran jagororin **Ahlulbaiti** a ko wane zamani su kan bayyana koyin da su ke yi da Sunnar magabata, musamman Abubakar da Umar. Amma a kullum in su ka faɗa, 'yan Shi'ah su kan ɗora maganarsu ne a ma'auninsu na munafurci (taƙiyyah), har su kan sa su rantse rantse. Misali, an tambayi Muhammad an Nafsuz Zakiyyah,

---

[40] Aj-Jamiu Li akhlaƙir Rawi wa adab as Sami', (1/546).

ko ka kan yi shafa akan huffi? Sai ya ce, e, ni kan yi. Ai Umar ɗan Haɗɗabi ya na shafa akan huffi. Sai mai tambayar (ɗan Shi'ah) ya ce masa, ba ruwana da Umar, ra'ayinka ni ke tambaya. A nan sai Muhammad ya fusata, ya ce, ba ruwanka da Umar? Umar kuwa ya fi cike da ƙasa irina. Sai mai tambayar ya ce ma sa, kana dai taƙiyyah ne. Sai ya ce, "To ka ga dai muna tsakanin ƙabarin Manzon Allah da mimbarinsa ko!, to, wallahi abin da na gaya maka, shi ne har a cikin zuciyata. Ya Allah ka sheda!.

Wani ma ya zo wurin Aliyyu ɗan Hussaini ya tambaye shi dangane da Abubakar ba tare da wata girmamawa ba. Sai ya ce, kana nufin Siddiƙ? Sai mai tambayar ya ce, kuma kai za ka kira shi Siddiƙ? Sai Aliyyu ya ce, waɗanda su ka fi ni ne su ka kira shi Siddiƙ, Manzon Allah (SAW) da Muhajirai da Ansarai. Duk wanda bai kira shi Mai gaskiya ba kada Allah ya gaskata zancensa duniya da lahira.

Ja'afar ɗan Muhammad as Sadiƙ ya na cewa, Wallahi Ni ina jiɓintar Abubakar da Umar, ina ƙaunarsu. Idan ba haka ne ba

Ya Allah! kada ka sa ceton Muhammadu (SAW) ya same ni.

Kuma shi ne ya ke cewa: Duk wanda ya barranta daga Abubakar da Umar, ni ma na barranta daga gare shi.[41]

### 3.3.2 Ahlulbaiti su na sanya wa 'ya'yansu Sunayen Sahabbai

soyayyar da ke tsakanin **Ahlulbaiti** da Sahabbai, ta sa an wayi gari, suna zana ma 'ya'yansu sunayen manyan Sahabbai. Misali:

Ga sunayen manyan 'ya'yan Sayyiduna Ali (RA):

- Al-Hassan
- Al-Hussaini
- Muhsin
- Muhammad
- Abubakar
- Umar
- Usman

[41] Duba duk waɗannan maganganu da mu ka cirato a cikin littafin: Aƙa'idus Shi'ah fil Mizan, na Dr. Kamaluddin al Hashimi, Shafi na 132-133.

Daga cikin ‘ya’yan Abdullahi ɗan Ja’afaru akwai :

- Abubakar
- Mu’awiyya

Daga cikin ‘ya’yan Mu’awiyya ɗan Abdullahi ɗan Ja’afar akwai :

- Yazidu

Daga cikin ‘ya’yan Hassan ɗan Ali (RA) akwai :

- Abubakar
- Umar
- Ɗalhatu

Daga cikin ‘ya’yan Hussaini ɗan Ali (RA) akwai :

- Abubakar (Zainul-Abidin)
- A’ishah

### 3.3.3 Ahlulbaiti na auratayya a tsakaninsu da Sahabbai da Tabi’ai

Kaunar da ke tsakanin **Ahlulbaiti** da Sahabbai da Tabi’ai, ba ta taƙaita kawai akan abin da ya gabata ba, har ma akwai

aurataүya a tsakanin gidajensu. Su ka zama abu ɗaya, sashensu ya haɗe da sashe. Wannan kuwa babu shakka ba zai yuwu ba in babu fahimta da mutunta juna. A nan za mu kawo wasu daga cikin amarmarin da tarihi ya tabbatar don kafa sheda akan wannan batu:

1. Manzon Allah (SAW) ya auri ɗiyar Abubakar da ta Umar (RA). Ya kuma aurar da 'ya'yansa mata guda uku (Zainab da Ruƙayyah da Ummu Kulsum) ga dangin Banu Umayyah. Zainab ta auri Abul Asi, Su kuma biyun su nauri Sayyiduna Usman.

2. Umar (RA) ya auri Ummu Kulsum ɗiyar Faɗimatu da Ali (RA).

Ko da ya ke babban malamin Shi'ah al Kulini a cikin littafinsa al Kafi ya ruwaito daga Abu Abdillahi Ja'far as Sadiƙ (A.S) cewa, "wannan aure, shi ne farji na farko da su ka ƙwace mana".[42]

Wannan ruwayar ta kulini kuwa, tare da ban dariyarta, ta na da ban mamaki. Domin mun samu a sauran littafan Shi'ah abin da ya ke tabbata ma na cewa, Sayyiduna Umar ba ƙwacen wannan

[42] Furu'ul Kafi, na Kulini, 2/141.

yarinyar ya yi ba daga gidan Sayyiduna Ali. Kuma bai isa ya yi hakan ba, domin duk a cikin halifofi ba ɗan babban gida irinsa, kuma danginsa ba za su bari a yi masu irin wannan cin mutunci ba. To, ga ma dai Ibnu Abil Hadid (ɗaya daga cikin hujjojin Shi'ah) ya na hikaito ma na a cikin littafinsa Sharhin Nahjul Balagah cewa :

Wata rana Umar (RA) ya aika da wani saƙo zuwa ƙasar Ruma, sai Ummu Kulsum 'yar Ali ta sayi kwalbar turare biyu, ta ba wanda aka aika domin ya kai wa matar Sarkin Ruma kyauta. Da ɗan saƙo ya dawo, sai ya zo mata da kwalaben biyu a cike da Jauhari, daga matar Sarkin. Ummu Kulsum ta zazzage Jauharin a kan tabarma, tana kallo, tana murna, sai ga Umar (RA) ya faɗo a cikin gida. Da ya tambaye ta inda ta samu wannan Jauhari, sai ta kwashe duk labarin ta gaya masa. Sai Umar ya ƙwace Jauharin yace, haƙƙin Baitul Mali ne. ita ko tace: a'a, nata ne, don tukuici ne aka ba ta a sakamakon kyautar da ta aika wa matar Sarkin Roma. Har ma ta kafa ma sa hujja da cewa, ai Manzon Allah (SAW) ya kan amshi kyauta daga mutane, har daga sarakuna

kuma ya ba su tukuici. Umar ya ce, me ya sa ba ki tada naki manzo na musamman ba? Wannan ɗan saƙo na gwamnati ne, ba naki ne ba. Daga ƙarshe dai, a cewar wannan ruwayar, sai da Umar ya gayyato babanta Sayyiduna Ali (RA) don ya yi ma su hukunci. Kuma da Ali ya saurari bayanansu sai ya yi hukunci da cewa: Daga cikin Jauharin nan, a keɓe mata daidai iya kuɗin turarenta da ta aika. Saura kuma a saka a baitul mali, don ɗan saƙon da ta aika ya je ne a cikin dukiyar baitul mali, ba a cikin dukiyarta ba.[43]

To, duk da ya ke, wannan Malami ya kawo wannan labarin ne don ya yi suka ga Sayyiduna Umar (RA), wai ya ƙuntata ma jikanyar Manzon Allah (SAW), mu a nan mu na son mu jawo hankalin mai karatu ne da cewa, ya ya za'a yi mutum ya ƙwaci ɗiyarka, sannan ya neme ka don sulhu idan sun samu rashin fahimta da ita? Kuma idan Umar ya na da laifi a wannan hukuncin, alƙalin fa? Bari dai mu je gaba a taƙaice mu cika alƙawarin da mu ka yi na jeranta ma ka

[43] Sharhin Nahjul Balagah, na Ibnu Abil Hadid, (4/575).

amarmarin da suka gudana a tsakanin gidajen Sahabbai da na **Ahlulbaiti.**

3. Mu'awiyah ɗan marwan ɗan Hakamu daga cikin Banu Umayyah, shi kuma ya auri Ramlatu 'yar Ali ɗan Abu Ɗalib.

4. Walidu ɗan Abdul Muɗɗalibi ɗan Marwan ɗan Hakamu daga Banu Umayyah ya auri Zainab 'yar Hassan ɗan Hassan ɗan Ali.

5. Abdullahi ɗan Amru ɗan Usmanu ɗan Affan, daga Banu Umayyah ya auri Faɗimatu 'yar Hussaini ɗan Ali.

6. Abdullahi ɗan Zubairu ɗan Awwam, daga cikin ƙananan Sahabbai ya auri Ummul Hassan 'yar Hassan ɗan Ali.

7. 'yar'uwarta kuma, Ruƙayyatu 'yar Hassan ɗan Ali, ta auri ɗan'uwansa, Amru ɗan Zubairu ɗan Awwam.

8. Mus'abu ɗan Umairu daga cikin Sahabbai Muhajirai, ya auri Sukainah 'yar Hussaini ɗan Ali. Bayan rasuwarsa kuma ta auri Zaidu ɗan Umar ɗan Usman ɗan Affanu daga Banu Umayyah.

9. Hussaini ƙarami ɗan Zainul-Abidin ɗan Hussaini ɗan Ali, ya auri

Halimatu ‘yar Hamza ɗan Mus’abu ɗan Umairu.

10. Ummu Kulsum kuma, ‘yar Abdullahi ɗan Ja’afaru ɗan Abu Ɗalib, ta auri Abanu ɗan Usmanu ɗan Affan daga Banu Umayyah.

11. Marwanu ɗan Abanu ɗan Usmanu ɗan Affan daga Banu Umayyah, ya auri Ummul-Kasim ‘yar Hassan ɗan Hassan ɗan Ali.

12. Yazidu ɗan Mu’awiyah ɗan Abu Sufyan daga Banu Umayyah, ya auri Ummu Kulsum ‘yar Abdullahi ɗan Abbas (RA) suka haifi, Umar da Abdullahi.

13. Walidu ɗan Utbata ɗan Abu Sufiyyanu daga Banu Umayyah, ya auri ‘yar uwar Ummu kulsum ɗin, Lubabatu ‘yar Abdullahi ɗan Abbas.

Wannan abin da mu ke iya kawowa kenan daga cikin auratayyar dangin Manzon Allah (SAW) da sauran gidajen Sahabbai. Kuma mun ba da kulawa ta musamman ga dangin Banu Umayyah saboda mai karatu ya ƙara tabbata ƙaryar jita jitar da ‘yan Shi’ah su ke yaɗawa cewar akwai adawa da gaba a

tsakanin wannan dangin da ‘yan gidan Manzon Allah (SAW).

# BABI NA HUƊU

# 4.0 AHLULBAITI A WURIN RAFILAWA

Wannan babi zai yi bayani ne, a kan irin yadda Rafilawa (‘Yan Shi’ah) suka raba ɗaya biyu; suka ware wasu daga cikin **Ahlulbaiti,** suka goya su a bayansu, saura kuwa suka sanya su, ƙarƙashin duga-dugansu, suna taki. Duk ta hanyar amfani da ƙaryace – ƙaryace, don ɗaukaka darajjar wancan kashi da daƙushe ta wannan.

## 4.1 SU WANE NE AHLULBAITI A WURINSU?

Mun yi bayani a baya cewa, ‘yan shi’ah sun ware mutane huɗu daga cikin Ahlulbaiti su ka yarda da shigar da su a cikin **Ahlulbaiti** a yayin da su ka kori sauran danginsa baki ɗaya daga wannan martaba. Ga sauran bayani:

## 4.2 ‘Yan Shi’ah sun raba ɗaya biyu:

Bayan Rafilawa sun raba taron **Ahlulbaiti** zuwa gida biyu, wato ‘yan bora da ‘yan mowa, sai suka riƙi kashi na farko

da tawai da goyo, kashi na biyu kuwa da zagi da dangwara.

### 4.2.1 **Ɓangare na farko a wurinsu: 'Yan Mowa**

Rafilawa sun kai matuƙa, har da wuce wuri, a cikin girmama, waɗanda suke ganin su ne **Ahlulbaiti** na haƙiƙa. Sun yi imani da cewa, waɗannan mutane ba su kuskure; duk abinda suka aikata daidai ne (Ma'asumai kenan). Kamar yadda Al-majlisi ya faɗa a cikin littafinsa Biharul-Anwar, "Ka sani Shi'ah Imamiyyah sun yi ittifaƙi akan tsarkakuwar Imamansu daga yiwuwar aikata zunubbai manya da ƙanana. Allah ya tsarkake su tun azal. A cikin littafin hisabinsu, babu kuskure ko ganganci ko mantuwa ko talalaɓiya a wajen fassara, ko rafkanwa daga wurin Allah; Duk abinda suka aikata daidai ne.[44]

[44] Biharul-Anwar, (9/205). Kuma ka duba irin wannan magana, a cikin littafansu kamar haka: Kashful Muradi, Sharhin Tajridul I'tiƙadi na Hilli (90), da Ikmaluddin na as Saduƙ (474) da Aƙa'idul Imamiyyal Isna Ashriyyah na Zanjani (2/157) da Aƙa'idul Imamiyyah na Muzaffar (104) da Al-Hukumatul Islamiyyah, na Khumaini (19).

Amma kuma ai Allah (SWT) cewa ya yi, mu koma ga Manzonsa, a duk lokacin da muka kasa jittuwa a tsakaninmu.[45] Da kuwa akwai wani mutum tsarkakakke daga aikata kure bayan Manzo, to, da kuwa Allah ya Umurce mu da tuntuɓarsa a lokuttan saɓani.

Rafilawa ba su tsaya ga raya cewa, Imamansu ba su kuskure ba, wanda hakan ke daidaita kafaɗar Imaman, da ta Annabawa. Sun ma tafi a kan cewa Imaman nasu, sun fi gaba ɗayan Ananabawa da Manzanni daraja ninkin baninki. Al Majlisi na da baboba na musamman, a cikin wannan littafi nasa, a kan haka, kamar: Babin fifikon Darajar Imamai (AS) akan Annabawa da dukan halittu. Ya kawo **Ruwaya** tamanin da Takwas, a ƙarƙashin wannan babi, waɗanda dukansu ƙiran ƙarya ne ga Manzon Allah (SAW). Akwai kuma babi akan cewa, Imamai na da ɗaukaka da matsayi irin na Manzon Allah (SAW); da shi da su ba banbanci.

Shi kuwa Al-mufid, cewa ya yi, a cikin Rasa'il nasa: "kasancewar Sayyiduna Ali (RA) halitta mafi soyuwa a wurin Allah,

45 Suratun Nisa'i: 59

na tabbatar da cewa shi ne, mafifici a kansu (Annabawa). Wannan kuma na nuna cewa ya fi su wurin Allah. Shi ne kuma limamin masu bautar Allah. Kai a taƙaice dai, duk wani abinda Allah ya halitta yana bayansa ga daraja, a wurin Allah, kamar dai yadda muka faɗa, har Annabawa da Mala'iku duk suna bayansa".[46]

Karewa da ƙarau ma, daga cikin littafansu, akwai littafin "Tafdhilul – A'immati Alal Anbiya'i", "Fifitar da Imamai akan Annabawa" wanda malaminsu mai suna, Hashimu ɗan Sulaiman Al Bahrani daga cikin malamansu na ƙarni na sha ɗaya ya wallafa. Kuma ma'anar da ke cikin wannan magana ce, Khumaini ya tabbatar, a cikin wancan littafi nasa. inda yace : "yana cikin shika-shikan mazhabarmu, imani da cewa Imamanmu na da wani matsayi da, babu wani Mala'ika makusanci, ko Annabi da aka aiko, da ya isa ya same shi".[47]

---

[46] Rasailul Mufid, Shafi na 37.

[47] Al Hukumatul islamiyyah, na Khumaini, Shafi : 51.

Rafilawa ba su tsaya nan ba, sai da aka wayi gari, su na ba Imamansu irin siffofin da sai Allah (SWT) ne kawai, ke da su. Kamar rayawarsu cewa, Imamai na karɓar addu'a. Da kuma imani da cewa, Imamai sun san gaibi; sun san duk abinda ya faru a duniya, da wanda ke faruwa, da wanda zai faru, har ranar ƙarshe. Haka kuma wai, duk abinda ke cikin zukatan 'yan adam sun san shi, har ma da abinda ke cikin tsatson maza da mata kafin su haife shi. Kuma sun san da 'yan Aljanna da 'yan Wuta, kuma babu ma wanda zai shiga Aljanna sai sun sa masa hannu. Sa'annan suna da ikon yin duk yadda suka so da halitta, ko su warkar da makaho da kuturu, ko su tayar da matacce da sauransu.[48]

Ya zo a cikin littafin Usulul-Kafi, Kitabul Hujjah, cewa, su dai "Imamai su na

[48] Duka waɗannan su na nan a cikin littafin kafi, wanda su ka fi dogara a kansa bisa ga ko wane littafi. Haka ma akwai su a cikin littafin Uyunul Mu'jizati, na Hussaini ɗan Abdul Wahhab, ɗaya daga cikin malansu na ƙarni na biyar.

da haƙƙin halatta abinda suka ga dama, su kuma haramta abin da suka ga dama"[49]

### 4.2.2 Reshe ya jirkice da mujiya

Wani lokacin ma, sai ka taras da su, a ƙoƙarin ɗaukaka darajar Imaman nasu, suna tozarta su, har abin ma ya kan zama tozartawa ga Manzon Allah (SAW) ɗin kansa. Idan ka karanta littafin Al-Ihtijaj, na Ɗabarsi, da littafin Sulaimu ɗan ƙaisu, da babin farko daga littafin "A'yanush Shi'ah", to, za ka ga irin yadda suka kitsa wani rikici na ƙarya a tsakanin Nana Faɗimatu (RA) da Surukan babanta, Abubakar da Umar (RA). Wai ta tarar da su a kasuwa ta nemi haƙƙin gadonta na gonar Fadak wacce Manzon Allah (SAW) ya bari, ta tsaurara mu su magana har ta kai ga ɗaga murya, a cikin dubu, ta kuma yi barazanar ɗebe mayafinta. Kuma wai, a sanadiyyar wannan matsala ne, su Umar suka ƙone ɗakinta, suka karya mata haƙarƙarinta, har ta yi ɓarin cikin da ta ke ɗauke da shi tun a zamanin Manzon Allah (SAW). Kuma duk abin nan da ke faruwa, shi Ali (RA) ya na tsaye yana kallo, bai iya

[49] Usulul-Kafi, Kitabul Hujjah, shafi na 278.

ce ma su tin ƙanzil, sai dai kawai ya yi ta rarrashinta, ya na ba ta haƙuri.50

Haba Malaman Shi'ah! Duk akan abin duniya?! Ashe ba Manzo ne da kansa ba (SAW) ya ke roƙon Allah, ya na cewa: "Ya Ubangiji ka sanya arzikin iyalina ya zamo kadaran kadahan"?. Ba kuma shi ne, ya ke cewa ba, Ya Allah! ka rayar da ni talakka, ka kashe ni a talakka, ka kuma tayar da ni a cikin talakkawa? To, ya aka yi 'yarsa ta zo ta na wannan cin mutunci ga surukanshi akan abin duniya?! Shin ita kaɗai ce ta ke da haƙƙen gadon ne? Su ban da 'ya'yansu da su ke matayen Manzon Allah? Ina baffansa Abbas? Shi ma ba ya gado ne? Ko duk sun bar ta ne ta nemo mu su haƙƙensu daga azzalumai? Ku sake duba ruwayoyin naku dai don Allah!!.

Haka kuma a cikin littafin: Furu'ul-kafi na Kulini da Jala'ul Uyuni na Majlisi, sun raya cewa, wai Faɗimatu (RA) ta ƙyamaci aurenta da Ali (RA), a kan wai sadakin da ya ba ta, bai taka kara ya karya

---

[50] Al-Ihtijaj, na Ɗabarsi, shafi na 145. da littafin Sulaimu ɗan ƙaisu, Shafi na 253, babi na farko: "A'ayansh-Shi'a", shafi na 26,

ba. Har sai da Manzon Allah (SAW) ya yi ta rarrashinta, da cewa: "Ba fa ni ne nike umurninki da auren Aliyu ba; Allah (SWT) ne yayi umurni da hakan daga sama". To, sa'annan sai ta miƙa wuya.[51]

### 4.2.3. Kazamtattun Ruwayoyin Shi'ah a game da Ahlulbaiti

Akwai kuma daga cikin ƙazamtaccin ruwayoyinsu, abinda mai littafin" Ilalush Shara'i' ya kawo, cewa wai, wata rana an tambayi Manzon Allah (SAW) cewa, wai me ya sa, muka ga ko da yaushe, kana sumbuntar Faɗimatu, kana kuma kusantowa da ita gare ka, ka na rungumarta? Sai ya ce, "Ina haka ne don ina jin tana ƙanshin aljanna. Wannan kuwa ya faru ne, saboda an samu cikinta ne sanadiyyar wani aful da Jibirilu ya zo mani da shi daga cikin aljanna, wanda kuma na ci, ya bi jinin jikina, a ranar ne kuma na kwanta da Khadijatu sai ta samu cikinta".[52]

---

[51] Furu'ul-kafi na Kulini (2/157) da Jala'ul Uyuni na Majlisi, shafi na 61.

52 Ilalush Shara'i' (1/183).

Daga cikin ƙoƙarinsu na bayyana fifikon Ali da 'ya'yansa da abin da ya ke fifita su akan Manzon Allah (SAW) akwai ruwayar da Ibnu Rajab al Bursi ya kawo a tafsirinsa Al Burhan cewa, wai a lokacin da aka yi Mi'raji da Manzon Allah (SAW) zuwa sama, ko da ya isa ya taras da Ali (RA) da 'ya'yansa Hassan da Hussaini.[53]

Akwai kuma ruwayar da Arbili ya kawo a cikin Kashful Gummah cewa, Allah ya yi magana ne da Manzonsa a lokacin da ya yi Mi'raji da irin muryar Ali, har sai da Manzo ya tambayi Ubangiji cewa, "Shin kai ne ka ke magana da ni, ko Ali?".[54]

Irin sukar lamirin da Manzo da Iayalan gidansa, ke gamuwa da shi, a sakamakon shishshigi da wuce iyakar Rafilawa, baya da iyaka. Ya zo a cikin Tafsirin Al Burhan har wa yau, cewa, wai wata rana Annabi (SAW) ya kwatse A'ishah (RA) saboda ta nuna fushinta ga abinda Ali (RA) ya yi, na zaunawa tsakaninta da

53 Al Burhan (2/404).

54 Kashful-Gummati (1/106).

Manzon Allah, har shi Alin ya hau kan cinyarta.[55]

A wata ruwaya ma sun nuna cewa, Manzon Allah ne, ya umurci Ali (RA) da ya zauna a bayansa, alhali kuwa, ita A'ishah, tana wurin. Sai shi kuma Ali ya sunkuyar da bayansa har sai da ya shafi ƙirjinta. A nan ne ta fusata har ta yi masa magana. Sai Manzon Allah (SAW) ya kwatse ta da cewa, "kar ki cuta min ga ɗan uwana".[56]

A nan kuma ga wata ruwaya da ni ke fatar mai karatu ya yi haƙuri da irin rashin kunyar da ta ƙunsa. Malamai sun ce, ba da labarin kafirci ba kafirci ba ne. Ba don haka ba Wallahi ba mu hikayar waɗannan al'marori. A cikin Biharul Anwar, ɗaya daga cikin mafi darajar littafan Shi'ah, kuma mafi girmansu, ga abin da suka ruwaito daga Ali (RA): "Mun yi wata tafiya ni da Manzon Allah (SAW), a cikin ayarin har da A'ishah. Ni kaɗai ne kuma ni ke yi masa hidima. Shi kuma Manzon Allah (SAW) ya na da wani mayafi guda tilo. Saboda haka ya kan yi bacci a tsakanina da A'ishah, mu duka uku

55 Tafsirin Al Burhan, (4/225).

56 Littafin Sulaimu ɗan Kaisu, Shafi na 179.

ba mu da wani mayafi in ba shi ba. Idan Manzon Allah (SAW) ya tashi a cikin dare, sai ya kan sanya hannunsa ya shaya sitira akan mayafin, a tsakanina da A'ishah.[57]

### 4.2.4. Sama ta koma ƙasa

Ga kuma wasu hadissai a wurin Shi'ah da zasu bayyana ma na gwargwadon darajar da **Ahlulbaiti** su ke da ita a gurinsu, ta yadda sai an yi jan aiki kafin a cimma wannan darajar. A cikin "Tafsiru Manhajis Sadiƙin" na Kashani, wai Annabi (SAW) ya ce: "Duk wanda ya yi auren mutu'a sau ɗaya, ya yi daidai da darajar Hussaini. Wanda kuwa ya yi auren mutu'a sau biyu, ya yi daidai da darajar Hassan. Wanda kuwa ya yi auren mutu'a sau uku, ya yi daidai da darajar Ali. Wanda kuwa ya yi auren mutu'a sau huɗu daidai yake da darajata.[58]

A wasu littafan Shi'ah, Manzon Allah (SAW) bai wuce darajar sauro ba, ko kuma ya ɗan ɗara shi kaɗan. Ga abin da aka ce a cikin Tafsirin al Kummi da na Ayyashi da littafin Sulaimu ɗan ƙaisu, game da wannan ayar:

---

57 Biharul Anwar (2/40).

58 Tafsiru Manhajis Sadiƙin, na Kashani 2/493.

Allah Ta’ala na cewa :

﴿ إِنَّ اللَّهَ لَا يَسْتَحْيِي أَنْ يَضْرِبَ مَثَلًا مَا بَعُوضَةً فَمَا فَوْقَهَا ﴾

**“lalle ne Allah ba ya jin kunyar bayyana wani misali, ko wane iri ne, sauro da abinda yake sama gare shi” [surar Baƙara:26].**

Sauron nan Allah na nufin Ali (RA) ne. abin da ke sama gare shi kuwa Manzon Allah.[59]

## 4.2.5. ‘Yan Shi’ah su na zuƙa ma Ahlulbaiti ƙarya

Daga cikin ƙaryace-ƙaryacen da waɗannan mutane, ke yi wa **Ahlulbaiti**, akwai wata ruwaya, ta Mullah Muhammad kazim, a cikin: Ajma’ul Fadha’ih, wadda ya ce ya karɓo daga Abu Hamza Al Sumali, shi

---

[59] Duba: Tafsirul Kummi (1/30) da Tafsirul Ayyashi (1/25) da littafin Sulaimu ɗan ƙaisu, shafi na 130.

kuma ya ji daga Zainul Abidin, cewa: “Duk wanda ya la’anci gumaka biyu (Yana nufin Sayyiduna Abubakar da Umar (RA) la’ana ɗaya, Allah zai rubuta masa lada dubu sau dubu saba’in (Miliyan Saba’in kenan), ya kuma shafe masa zunubi dubu sau dubu saba’in (Miliyan Saba’in kenan), ya kuma ɗaukaka darajarsa mataki dubu sau dubu saba’in (Miliyan Saba’in kenan). Duk wanda kuma ya maraita yana la’antar su, la’anta ɗaya, zai samu irin wancan sakamako.

To, daga nan sai Maulana Aliyu ɗan Hussaini yace, “Na tafi wurin Maulana Abu Ja’afar Muhammad al Baƙir, nace masa me nene gaskiyar wannan Hadisi da na ji daga mahaifinka?. Sai ya ce in karanta Hadisin. Da na karanta sai ya ce, “Ai ba iyakar hadisin ke nan ba. Bari ka ji cikonsa. “Duk wanda ya la’ance su, la’anta ɗaya a kowace safiya, duk abinda ya aikata Allah ya yafe masa, har rana ta faɗi. Wanda duk kuwa ya la’ance su, la’anta ɗaya da marece, duk laifin da ya aikata, ba za a rubuta masa zunubi ba har a wayi gari”.

Daga nan kuma na shiga wurin Maulana As Sadiƙ. Shi ma muka yi yadda

mu ka yi da Al Baƙir da shi. Yace mi ni, "Tabbas haka ya ke" har ya ƙara da cewa, "Allah kuma zai ɗaukaka darajjarsa mataki dubu sau dubu biyu (Miliyan biyu kenan). Wannan duk ba abu ne mai wuya ga Allah ba".[60]

### 4.3. Ɓangare na biyu na Ahlulbaiti a wurinsu: 'Yan bora

A ɗayan ɓangare kuma, Rafilawa sun yi tsananin wuce iyaka, a cikin ƙasƙanta darajar wasu daga cikin iyalin gidan Manzon Allah (SAW) da suka haɗa da, matansa (Uwayen Muminnai) da sauran 'ya'yansa, in ban da Fatima, da kusan dukkan danginsa na Banu Hashim in ban da Ali.

#### 4.3.1. Matan Manzon Allah (SAW) da Ubannensu

Babu ɗaya daga cikin waɗanda muka lissafa a baya, wanda ya tsira daga kafircin da Rafilawa ke jifar Sahabban Manzon Allah (SAW) da shi. Sun ma ɗauka cewa, zagi da la'antar da suke yi wa waɗannan bayin Allah, na ɗaya daga cikin manya-

---

[60] Diya'us Salihin, Shafi na 513.

manyan ayyuka, managarta da ke kusantar da mai yin su ga Allah. Har ma Mashahurin malaminsu As Saduƙ ya ruwaito, a cikin: Ikmalud Din, cewa, wai Manzon Allah, ya danƙa wa Ali damar sakin matansa ko bayan rayuwarsa, yace masa, duk wadda ta tsangwame ka ko a bayan raina ne na yi maka izni ka sake ta.[61]

Bari ka ji, abinda Al Majlisi ke cewa a cikin "Haƙƙul Yaƙini", a ƙoƙarinsa na bayanin aƙidarsu: "Imanin mutum a wurinmu, ba ya inganta, sai ya raba gari (Bara'a) da gumaka huɗu: Abubakar da Umar da Usman Ma'awiyah. Ya kuma raba gari da mata huɗu: A'ishah da Hafsah da Hindu da Ummul-Hakam. Ba su kaɗai ba. Kai sai ya raba gari da duk wani mai ƙauna da biyayya gare su. Sai kuma ya ƙudurce cewa, su ne mafi sharrin halitta a bayan ƙasa. Don kuwa mu, a wurinmu, waɗannan mutane, su ne manyan maƙiyan Allah da Manzonsa, da Imamai".[62]

Haka kuma, Al Kashani, ya tafi akan cewa; matar Nuhu da ta Luɗu, waɗanda

---

[61] Ikmalud Din, na Saduƙ, Shafi na 429-430.

[62] Haƙƙul Yaƙini, na Majlisi, Shafi na 159.

Allah (SWT) ya buga misali da su, a cikin Al-ƙur'ani, in da ya ke cewa,

﴿ضَرَبَ اللَّهُ مَثَلًا لِلَّذِينَ كَفَرُوا امْرَأَةَ نُوحٍ وَامْرَأَةَ لُوطٍ كَانَتَا تَحْتَ عَبْدَيْنِ مِنْ عِبَادِنَا صَالِحَيْنِ فَخَانَتَاهُمَا فَلَمْ يُغْنِيَا عَنْهُمَا مِنَ اللَّهِ شَيْئًا وَقِيلَ ادْخُلَا النَّارَ مَعَ الدَّاخِلِينَ﴾[التحريم: ١٠].

Allah Ya buga misali ga waɗanda su ka kafirta, Matar Nuhu da Matar Luɗu. Sun kasance a ƙarƙashin bayi biyu daga cikin bayinmu na kirki, sai su ka yaudare su. (Wannan) bai wadatar mu su da kome ba daga Allah. Sai aka ce (mu su) "ku shiga

wuta tare da masu shiga (cikinta)”.

Surar Tahrim aya ta 10.

Wai in ji Kashani anan Allah ya yi arashi ne. Kuma a haƙiƙa, ana wanka da kamar jurwaye ne ga A'ishah da Hafsah. Domin Allah (SWT) ya yi haka ne, a cewarsa, don ya bayyana irin cin amanar da waɗannan mata suka yi wa Manzon Allah (SAW) ta hanyar munafuccin da suka rinƙa ƙulla masa, tare da kasa shi a faifai, da kuma yin fito-na-fito da shi.[63]

Babban cin mutuncin da suka yiwa A'ishah, duk bai fi, zarginta da suka yi da cewa, wai ta yi karuwancin har ta haɗa dinari arba'in, don ta taimaka wa magabta nali (RA) da su. Ibn Rajab Al Bursi, a cikin littafinsa Mashariƙu Anwaril Yaƙini, shi ya furta wannan ƙazamar magana.[64]

---

[63] Tafsirin As Safi na al Faid al Kashani (2/720). A haƙiƙanin gaskiya, kusan ijma'i ne a tsakanin malaman Rafilawa game da kafirta Sayyidah A'ishah. Za mu ga wannan ko ina a cikin rubuce-rubucensu. Duba alal misali: Biharul Anwari na Majlisi (22//33) da As Siraɗul Mustaƙim na Bayadi (3/165-166) da Aƙa'idul Imamiyyah na Zanjani (3/89).

[64] Mashariƙu Anwaril Yaƙini, na Bursi, shafi na 86.

A nan dole ne mu tunatar da mai karatu abin da Allah (SWT) yace game da, waɗanda su ka zargi A'ishah tun da farko:

﴿ يَعِظُكُمُ اللَّهُ أَنْ تَعُودُوا لِمِثْلِهِ أَبَدًا إِنْ كُنْتُمْ مُؤْمِنِينَ﴾ (النور:١٧)

**"Allah yana yi muku wa'azi, kada ku koma ga irinsa, har abada, idan kun kasance muminai"**

**[Surar Nur :17]**

ya kuma ce, a kan waɗanda suka yi mata ƙazafi:

﴿إِنَّ الَّذِينَ يَرْمُونَ الْمُحْصَنَاتِ الْغَافِلَاتِ الْمُؤْمِنَاتِ لُعِنُوا فِي الدُّنْيَا وَالْآَخِرَةِ وَلَهُمْ عَذَابٌ عَظِيمٌ (٢٣) يَوْمَ تَشْهَدُ عَلَيْهِمْ أَلْسِنَتُهُمْ وَأَيْدِيهِمْ وَأَرْجُلُهُمْ بِمَا كَانُوا يَعْمَلُونَ (٢٤)

يَوْمَئِذٍ يُوَفِّيهِمُ اللَّهُ دِينَهُمُ الْحَقَّ وَيَعْلَمُونَ أَنَّ اللَّهَ هُوَ الْحَقُّ الْمُبِينُ (٢٥) الْخَبِيثَاتُ لِلْخَبِيثِينَ وَالْخَبِيثُونَ لِلْخَبِيثَاتِ وَالطَّيِّبَاتُ لِلطَّيِّبِينَ وَالطَّيِّبُونَ لِلطَّيِّبَاتِ أُولَئِكَ مُبَرَّءُونَ مِمَّا يَقُولُونَ لَهُمْ مَغْفِرَةٌ وَرِزْقٌ كَرِيمٌ (٢٦)﴾ [سورة النور].

“Lalle ne wadannan da suke jifar mata masu kamun kai gafilai, muminai, an la’ance su, a cikin duniya da Lahira kuma suna da azaba mai girma. A ranar da harsunansu, da hannayensu, da ƙafafunsu suke bayar da shaida a kansu, game da

abinda suka kasance suna aikatawa. A ranar da Allah ya ke cika masu sakamakonsu tabbatacce, kuma suna sanin (cewa) Lalle Allah, shi ne Gaskiya bayyananna. Miyagun mata domin miyagun maza suke, kuma miyagun maza domin miyagun mata suke, kuma tsarkakan mata domin tsarkakan maza suke, kuma tsarkakan maza domin tsarkakan mata suke. Waɗancan su ne, waɗanda ake barrantarwa daga

abinda (masu zargi) suke faɗa, kuma suna da gafara da arziki na kurumci".

[Surar Nur: 23-26]

Wani zargi kuma da su ka yi, shi ne cewa, wai, ita A'ishah da babanta, tare kuma da Hafsah da babanta su ne su ka kashe Manzon Allah, ta hanyar ba shi guba. Al-majalisi ne dai har wayau ya ke da zunubin wannan ƙarya a cikin littafinsa Hayatul ƙulubi.[65]

Zargi na gaba kuma shine, wai ita Nana A'ishar ta aurar da kanta ga Ɗalhatu ɗan Ubaidullahi[66], kuma har ya sadu da ita. Wannan ƙazafin shi kuma ya fito ne daga yawun alƙalumman Bahrani a cikin

---

[65] Hayatul ƙulubi, na Majlisi, babi na 55, (2/742).

[66] Ɗaya daga cikin mutane goma da Manzon Allah (SAW) ya yi mu su bushara da aljanna.

Tafsirinsa "Al Burhan" da Abdullahi Shabbar a cikin nasa tafsirin.[67]

### 4.3.2. Sauran 'ya'yan Manzon Allah (SAW)

Haka kuma, Rafilawa sun yi kakkausar suka, ga sauran 'ya'yan Manzon Allah (SAW), in ka cire Fatima, musamman dai matan. Lamarin ma har ya kai ga su tattauna ko ma Zainab da Ruƙayya da Ummu Kulsum, duk 'ya'yan Manzon Allah ne, ko a'a. Binciken wasu daga cikinsu dai ya ƙare akan cewa, agolayensa ne. ko dai Sayyida Khadija ce ta haifo abinta kafin aurenta da Manzon Allah (SAW), ko kuma ma riƙonsu ta ke yi. In kuma haka ne, to, 'ya'yan ƙanwarta ne, ko ko ma 'ya'yan wata mai hidimar gidanta ce kawai ta rasu ta bar mata su?.[68]

---

[67] Bahrani a cikin Tafsirinsa "Al Burhan" (4/358) da Abdullahi Shabbar a cikin nasa tafsirin, Shafi na 338.

[68] Duba wannan kace nace a tsakaninsu cikin: Al Istigasah Fi Bida'is Salasah, na Al Kufi, (1/64-76) da Ihƙaƙul Haƙƙi, na Tustari (250-251) da Aƙa'idul Imamiyyah, na Zanjani (3/43) da kuma As Siraɗul Mustaƙim, na Bayadhi (3/83).

To, ka dai ji irin sharholiyar malaman nasu. Amma duk da haka da yawansu sun yarda cewa, waɗannan bayin Allah ‘yan gidan Annabta ne, kuma Annabin da kansa ne ya haife su. Ko banza ma kore su ba ya iya karɓuwa ga duk wanda ya ke karanta Alƙur’ani don ko Allah ya faɗe su a cikin Suratul Ahzabi a dunƙule kamar yadda mu ka ambata can a baya.

To, sai dai waɗannan malaman Shi’ah da su ka yarda cewa, su Zainab ‘ya’yan Manzon Allah ne, sun sha wahala matuƙa wajen lalubo dalilin da ya sa Manzon Allah (SAW) ya aurar da su gaba ɗaya ga Banu Umayyah waɗanda, a wurinsu su ne, mafi nisantar mutane daga rahamar Allah!

Saboda tsananin rashin ganin girman ‘ya’yan Manzon Allah (SAW), da wannan ƙungiya ke yi, suka ƙirƙiri labarin cewa, wai Allah ya aiko wa Manzonsa, da cewa, ya zaɓi ɗaya, tsakanin ɗansa Ibrahimu da Jikansa Hussaini. Don ko Allah ba zai haɗa masa su gaba ɗaya ba. Har su kace wai, Manzon Allah (SAW) yace, wannan da ya ke ɗan baiwa? Cewa da ɗansa Ibrahim. Don

haka sai ya zaɓi Hussaini. Shi kuma Ibrahim Allah ya karɓi rayuwarsa.[69]

### 4.3.3 Sauran dangin Manzon Allah (SAW)

Sauran dangogin Manzon Allah (SAW), iyayensa da ƙannensa duk ba su tsira ba daga miyagun kalaman Rafilawa.

Abbas, wanda shi kaɗai ne baban Manzon Allah (SAW) da ya rage ma sa, kuma Manzon Allah (SAW) ya kasance ya na ba shi girma matuƙa, har ma ya kan ce, ba ku san baffan mutum matsayin babansa ne ba? Wannan Baffan na Manzon Allah (SAW) 'yan Shi'a sun yi ma sa jafa'i, daga shi har 'ya'yansa. Ko a gidan su Ali ma sai da su ka nuna wariya, don ko za mu ga irin tozartawar da su ke yi ma shaƙiƙinsa watau, Aƙilu ɗan Abu ɗalib.

A cikin littafin Kafi, an ce wai, Abbas da Aƙilu duk mutane ne masu raunin imani, ƙasƙantattu.[70]

---

[69] Biharul Anwar (22/153) da Manaƙibu Ali Abi Ɗalib (3/9234) da Isbatul Wasiyyah na Mas'udi, Shafi na 175.

[70] Al Kafi, 8/105.

Haka kuma, Al Kummi ya faɗa, a cikin tafsirinsa cewa; wai Sayyiduna Ali (RA) ya ce, ayar nan wadda Allah (SWT) ke cewa:

﴿ وَمَنْ كَانَ فِي هَذِهِ أَعْمَى فَهُوَ فِي الْآَخِرَةِ أَعْمَى وَأَضَلُّ سَبِيلًا﴾ (الإسراء:٧٢)

**"Kuma wanda ya kasance makaho a cikin wannan (duniya), saboda haka shi a lahira makaho ne, kuma mafi ɓata ga hanya".**

**[Surar : Isra'i : 72]**

Da kuma ayar da Allah ya ke cewa:

﴿ وَلَا يَنْفَعُكُمْ نُصْحِي إِنْ أَرَدْتُ أَنْ أَنْصَحَ لَكُمْ إِنْ كَانَ اللَّهُ يُرِيدُ أَنْ يُغْوِيَكُمْ﴾ (هود:٣٤)

**“kuma nasihata ba za ta amfane ku ba, idan na yi nufin in yi muku nasiha, idan Allah ya kasance yana son ya halaka ku. [Surar : Hud : 34]**

Alƙummi ya ce, wai duk ayoyin nan, sun sauka ne kan Sayyiduna Abbas da ‘ya’yansa.[71]

Haka kuma a cikin Rijalul kashshi cewa su ka yi a inda Allah ya ke cewa:

﴿وَمِنَ النَّاسِ مَنْ يَعْبُدُ اللَّهَ عَلَى حَرْفٍ فَإِنْ أَصَابَهُ خَيْرٌ اطْمَأَنَّ بِهِ وَإِنْ أَصَابَتْهُ فِتْنَةٌ انْقَلَبَ عَلَى وَجْهِهِ خَسِرَ الدُّنْيَا وَالْآخِرَةَ ذَلِكَ هُوَ الْخُسْرَانُ الْمُبِينُ (١١) يَدْعُو مِنْ دُونِ اللَّهِ مَا لَا

[71] Tafsirul Kummi (2/23-24) da Tafsirul Ayyashi (2/503) da Al Ikhtisas na mufid, Shafi na 71-72.

يَضُرُّهُ وَمَا لَا يَنْفَعُهُ ذَلِكَ هُوَ الضَّلَالُ
الْبَعِيدُ (١٢) يَدْعُو لَمَنْ ضَرُّهُ أَقْرَبُ
مِنْ نَفْعِهِ لَبِئْسَ الْمَوْلَى وَلَبِئْسَ الْعَشِيرُ
(١٣)﴾ [سورة الحج]

**"...Lalle ne tir da shi ya zama majiɓinci, kuma tir da ya zama abokin zama!"**

Wai su ma waɗannan ayoyi, su na shaguɓe ne game da Abbas (RA).[72]

Haka kuma, Rafilawa sun ce, wai Abdullahi ɗan Abbas (RA) ya sace gaba ɗayan dukiyar da ke Baitil Malin Basrah, ya gudu a lokacin da yake gwamna a can, a ƙarƙashin halifancin Ali (RA). A kuma sakamakon haka ne, wai shi Ali (RA) ya roƙi Allah ya makantar da Ibnu Abbas. Kuma wai, hakan aka yi, inji su.73

---

[72] Rijalul Kashshi, Shafi na 54.

[73] Ikhtiyaru Ma'rifatir Rijal, na Tusi, Shafi na 53-70 da Ma'rifatu Akhbarir Rijal, na kashshi, Shafi na 40-41.

kai saboda tsananin ƙiyayyar da, Rafilawa ke yi wa zuri'ar Manzon Allah (SAW), suka gayyato Tatar zuwa Bagdad, hedikwatar halifancin Banul Abbas, daga cikin Banu Hashim dangin Manzon Allah (SAW). Da wannan goron gayyata ne, na Rafilawa, Tatar suka yi wa Bagadada kaca kaca a wancan karon[74]. Suka kashe musulmi sama da Miliyan ɗaya da dubu ɗari takwas da saba'in. Suka kuma kama mata da kananan yara maza Hashimawa, suka bautar da su.[75]

Karewa da ƙarau ma, duk da zuri'ar Sarkin musulmi Ali (RA) ba ta tsira daga ƙazafi da ƙagen Rafilawa ba. Sun ce wai Ja'afaru ɗan Ali ɗan Muhammadu ɗan Ali ɗan Musa ɗan Ja'afaru As Sadiƙ (ƙanen Al Hassan Al Askari, wanda su ka ce shi ne

---

[74] Wannan ya faru ne a shekara ta 656B.H., Sai ga shi kuma a yanzu ya sake faruwa, in da 'yan Shi'a su ka gayyato Amerika zuwa Bagadada a karo na biyu a Shekarar 2002M/1423B.H. su ka sake aikata irin ɗanyen aikin da kakanninsu su ka yi, bayan shekaru 767. Ga Allah mu ke kai ƙarar sharrinsu.

[75] Duba wannan Labarin a cikin littafin Al Bidayah Wan Nihayah, na Ibnu Kasir, (7/13) da Siyaru A'lam al Nubala' (23/180-181)

mahaifin Mahadinsu) wai maƙaryaci ne, ba a saurarensa.[76]

Haka kuma, a cikin littafin Tanƙihul Maƙali, Al Mamaƙani ya ce; Ja'faru As Sadiƙ ya ce, wai da Hassan ɗan Hassan ɗan Ali ɗan Abu Ɗalib ya rasu yana mazinaci, mashayin giya da cin riba, to da ya fi alheri a kan halin da ya rasu a kai na kafirci (ya na nufin yarda da halifancin Abubakar da Umar da Usman (RA).[77]

Kuma wai ɗansa Abdullahi shi ma maƙaryaci ne.[78]

Shi ma jikansa, wato Muhammadu ɗan Abdullahi (An Nafsuz Zakiyyah) wai shi ma maƙaryaci ne, ya kuma yi da'awar Imamah.[79]

A taƙaice, gaba ɗayan 'ya'yan Hassan da Jikokinsa da shi Hassan ɗin kansa, duk ba su da wata ƙima a idon Rafilawa. Laifinsu kuwa shi ne, Hassan ya kunyata 'yan Shi'a a da'awar da su ka yi cewa,

---

76 Biharul Anwar, (51/5).

77 Tanƙihul Maƙali, na Mamaƙani, (1/273).

78 Duba: Basai'rud Darajat, a waɗannan shafukan: 173,176,194.

79 Tanƙihul Maƙali, na Mamaƙani, (3/142).

halifanci haƙƙinsa ne na gado, sai ga shi ya sauka bisa ga sulhu, ya bar wa Mu'awiyah don neman zaman lafiya da kwantar da fitina.

# BABI NA BIYAR

## 5.0 Matsayin Ahlulbaiti game da Rafilawa

Wannan babi – na ƙarshe – zai yi tsokaci ne, a kan matsayin Rafilawa a wurin **Ahlulbaiti**, ta hanyar kawo wasu kalamai, a matsayin sheda daga bakin Sayyiduna Ali (RA) da 'ya'yansa Hassan da Hussaini (RA) da wasu daga cikin danginsu.

### 5.1 Matsayin Ali Ɗan Abu ɗalib

Matsalolin da Sayyiduna Ali (RA) ya fuskanta daga wajen 'yan Shi'a, suna da yawan gaske, tattare da kasancewarsu masu bugun gaban zamansu magoya bayansa. Wannan ba ɓoye yake ba, ga duk wanda ke ta'ammuli da littafin Nahjul Balagah. Ali (RA) na cewa a cikin wata huɗuba, daga cikin littafin, ya na mai addu'a: "Ya Allah! ka sani, na gaji da su, su ma sun gaji da ni, Allah ka ba ni waɗanda suka fi su kirki; ka ba su wanda ya fi ni rashin haƙuri da zafin hannu".

Ko kaɗan Sayyiduna Ali (RA) bai ji daɗin rayuwa da 'yan Shi'a ba. sun kasance

suna ƙulla masa mafi munin makirci, ta hanyar ƙawance da abokan gabarsa, a rubuce, da cin amanarsa a duk lokacin da ya danƙa masu amanar wani aiki (wilaya) ko dukiya.

Wannan kuwa shi ne dalilin da ya sa, masu kaifin basira daga cikin masoyan **Ahlulbaiti**, irin su; Abdullahi ɗan Abbas da Abdullahi ɗan Umar da Abubakar ɗan Abdurrahman ɗan Harisu ɗan Hishamu, suka ba Hussaini shawarar kada ya karɓa gayyatarsu. Kamar yadda kuma, sauran Tabi'ar nan Amratu ta hane shi a rubuce. Amma kuma abinda Allah ya yi, Annabi sai ceto.

Ibnu Kasir da wasu malamai sun Lissafa mutum ashirin (20) daga cikin zuri'ar Hussaini, waɗanda 'yan Shi'ah suka halaka ta hanyar yi masu; Iza-wawa-kwari, su haɗa su faɗa da wan-ƙarfi, daga cikin shugabanni.

Daga cikin waɗanda suka lissafa akwai: Zaidu ɗan Ali ɗan Hussaini. Wanda a sakamakon ɗaure masa ne da suka yi, aka ambace su da 'yan a ɗaure (Rafilawa). Sun sako shi gaba ne, don a yaƙi Sarkin

Musulmi Hishamu ɗan Abdul-Malik, halifan Banu Umayyah, sai shi kuma a naɗa masa gadon gidansu, a cewarsu. Amma sai da yaƙi ya kusa kankama, sai su ka neme shi da ya la'anci halifofin farko (Abubakar da Umar). Abin ya ba shi mamaki ainun, domin bai ga wata alaƙa tsakanin abin da ake ciki ba da abin da su ka neme shi. A dalilin ƙiyawarsa kuwa suka ɗaure masa, su ka zame jiki, su ka bari aka kashe shi. Allah Ya jiƙansa.

Mu dawo ga maganarmu. Daga cikin abubuwan da Ali (RA) ke faɗa a kansu, a kwai wata huɗuba, a cikin Nahjul Balagah, wadda a cikinta ya ke cewa: "Ashe ma ƙaryar jaruntaka ku ke yi, ba ku aje komai ba, sai feshi da fankama. Wallahi da ma dai ban taɓa ganinku ko jin labarinku ba, ya fi alheri gare ni, don saninku bai daɗa ni da komai ba, sai nadama da ƙasa a gwiwa. Allah dai ya la'ance ku, kun cika zuciyarku da miyakun baƙin ciki, kun balbala wa ƙirjina wutar sunu, kun ɓata mi ni suna, kun dagula min tunani kun tara min gajiya".[80]

---

[80] Nahjul Balagah, Shafi na 70-71.

A wata huɗubar kuma yake cewa: “ya ku mutanen da gangunan jikinsu ɗai ke wuri ɗaya, amma hankulansu na wurare daban – daban. Ku na da wani abin kariya bayan gidajenku, ko kuma da wani shugaba da za ku yi yaƙi bayansa ban da ni?! Wallahi dai na tabbata, ba wawa sai wanda ya yi uwar yaƙi da ku, wanda duk ya sa ku gaba ƙarshensa kunya. Duk kuwa wanda rabonsa ya zama ku, to wallahi an jefe shi da sungumin ragga. Daga yau ba ni ƙara yarda da maganarku, ba ni ƙara tunanin samun taimako daga gare ku. In kuwa don taƙamar ina da ku, to duk maƙiyana sun zama masoya. Na tabbata dai dole akwai wata maƙarƙashiya, mutanen can babu abin da su ka fi ku. Duk abubuwan da ku ke faɗa sun zama ƙarya, kuma har abada ba a mutanen kirki da ku. Ba abinda kuka aje sai kissa da munafucci”.

Ya kuma siffanta su a cikin wata huɗuba, da cewa su: masu yawan suka da zagin mutane ne, mazanbata kuma ‘yan baya. Komai yawansu na banza ne, don ko wane daga cikinsu tunaninsa daban.[81]

[81] Nahjul Balagah, Shafi na 176.

Tabbatattar magana dai itace, Rafilawa ba su fitar da maitarsu a fili zamanin Ali (RA) ba. don an ruwaito yana cewa : “babu wanda zai fifita ni a kan Abubakar da Umar (RA) face na yi masa hukuncin mai ƙazafi”. Cikakkiyar aƙidar Shi’anci ta bayyana ne a fili bayan wucewarsa. Yardar Allah ta tabbata a gare shi.

## 5.2 Matsayin Hassan Ɗan Ali (RA)

Shi kuwa Hassan ɗan Ali (RA) abinda yake cewa a kan ‘yan Shi’ar zamaninsa, ya haɗa da cewa: “Wallahi na dai fahimci Mu’awiyah ya fi min alheri akanku. Kun ce ku masoyana ne, amma ga shi kun shirya kasheni da ƙwace dukiyata”.[82]

A wani shafin kuma ya ce : “Wallahi na fi son in ƙulla amana da Mu’awiyah, ko da hakan za ta ci ni har ga gashi, bisa ga in yi fito-na-fito da shi ya kashe ni, gidana da zuri’armu su watse. Don wallahi na tabbata, da zan yaƙi Mu’awiyah kashina ya gama bushewa, idan kuma ya kama ni a hannu ya yafe min zai zama abin faɗi gare ni da Banu

[82] Al-Ihtijaj, na Tabarsi, Shafi na 145.

Hashim har abada. Don na tabbata Mu'awiyah da jikokinsa za su yi wa rayayyu da matattunmu dariya".[83]

Daga abin da ya gabata za mu iya fahimtar dalillan da su ka sa Hassan ya gwammace yin sulhu da Mu'awiyah. Ba wani abu ba ne, ban da sanin da ya yi cewa, 'yan Shi'ah za su tozarta shi don ba su iya fidda suhe wuta.

## 5.3 Matsayin Hussaini Ɗan Ali (RA)

Abin da ya faru ga Sayyiduna Hussaini ɗan Ali (RA) shi ne abin da muka riga mu ka ambata a baya game da jikansa zaidu. 'Yan Shi'ah dai sun yi ma sa ingiza-wawa-kwari akan sha'anin Banu Umayyah. Sun rubuta ma sa dubunnan wasiƙu a lokacin da ya ke Makka, su na neman ya zo wurinsu don su hamɓarar da gwamnatin yazidu, su ɗora shi akan gadonsa. Da farko da ya aika ƙaninsa Muslimu ɗan Aƙilu, ya samu rahoto mai daɗi na irin kyakkyawar tariyar da ya samu daga mutanen kufa. Bai fahimci cewa, munafurci ne ba sai bayan da ya iso, ya samu labarin cewa, ashe tuni sun

[83] Al Ihtijaj, na Tabarsi, Shafi na 148.

miƙa Muslimu ɗan Aƙilu ga hukumomi har ma an kashe shi.

Anan ne ya wayi gari, gaba kura baya siyaki, su kuma ‘yan Shi’ah su ka dare masa, su ka bar shi a hannun waɗanda ya fito yi musu tawaye, sojojin Banu Umayyah su ka yi sukuwar sallah a kansa, ya yi shahada ya na wanda ‘yan Shi’ah su ka zalunta. Ga abinda littafan Shi’ah su ka ruwaito ya na cewa a kan mutanen Kufa, bayan da su ka tozarta shi:

“Allah dai ya la’ance ku, ya tozarta ku, ya ƙasƙantaku. Kun nemi taimakonmu, mun kuma taimake ku. Karshe ku ka yi mana yankan baya; ku ka yaƙe mu da takobin da ke hannunmu. Ku ka sa mu ka zama kurar gardi a hannun maƙiya, ku ka zaɓe su, ku ka ba mu baya, tattare da ba su fi mu kyautatawa zuwa gare ku ba. Har abada babu wani abu na alheri da za su iya yi maku, kamar yadda mu kuwa ba mu taɓa cin amanarku ba. Boni kuwa zai tabbata gare ku, tun da ku ka ƙi mu, daidai lokacin da babarbaren takobi ke wasar yara a kammu. Ku tuna fa, ku ne ku ka neme mu bisa alƙawali, ku ka lallashe mu, ashe yaudarar

mu kuke son ku yi. Allah ya ɗebe ma ku albarka. Ba wani ɗagutu, a wannan al'umma bayan ku".[84]

---

[84] Al-Ihtijaj, na Tabarsi, Shafi na 145. Wannan ya na daɗa bayyana mana azurakancin 'yan Shi'ah a bukukuwan makoki da su ke yi ranar Ashura don tunawa da Hussaini. Waɗannan bukukuwan ma ba su da wani asali ko tushe kafin lokacin Sarki Mu'izzud Daulah, ɗaya daga cikin sarakunan Shi'ah, waɗanda su ka yi ƙaryar cewa, su dangin Nana Fatima ne, kuma tarihi ya ƙaryata su. Wannan Sarkin shi ne farkon wanda ya yi umurni da yin zaman makoki, a kan rasuwar Hussaini, a shekara ta 352 B.H., ya kuma tilasta wa mutanen Bagadada rufe shagunansu, da kife tukwanen abincinsu, don yin jerin gwano tare da yin koke – koke, don nuna baƙi ciki, a duk lokacin da ranar Ashura ta kewayo. Bayan haka ne Sauran Sarakunan wannan Daular ta Shi'ah da ake kira Faɗimiyyah su ka ɗaure ma wannan bidi'ah gindi, su ka kuma ƙara faɗaɗa bukukuwan da ake gudanarwa cikinta. Duk musulmin ƙwarai kuwa, ya san wannan sabga ta saɓa wa, abinda Allah (SWT) ya umurce mu da yi idan musiba ta sabka gare mu. Wato mu riƙa faɗar: **"Inna Lillahi Wa Inna Ilaihi Raji'un" [Surar Baƙara : 156].** Duba labarin yadda aka ƙago bukin makokin a littafin: Al Ibar, na Zahabi, (2/89) da Al-Bidayah Wan Nihayah, na Ibnu Kasir (11/259) da Al-khuɗaɗ, na Maƙarizi, (1/431).

## 5.4 Matsayin Sauran Ahlulbaiti (RA):

Maganar ɗaya daga cikin Ma'asuman 'yan Shi'ah ta ishe mu hujja, a wannan ɓangare. Ga abinda mai littafin Raudhah ya ruwaito daga ɗaya daga cikin Ma'asumansu: "idan ka duba 'yan Shi'armu, babu mutum ɗaya daga cikin wanda ba tantiri ba. Da kuwa za ka bincike su, ɗaya bayan ɗaya, za ka taras dukkansu murtaddai ne".[85]

Duk da haka dai 'yan Shi'ah su na ɗaukar duk wata gaskiya da, wani daga cikin magabatan malaman **Ahlulbaiti** ya faɗa, a matsayin taƙiyya ce (Kissa). Wanda hakan ke sa har su kan ba su rantsuwa, a kaikaice, kamar yadda mu ka riga mu ka gabatar a baya.

## 5.5 Naɗewa:

Sanin **Ahlulbaiti** da matsayinsu ga al'ummar musulmi na ɗaya daga cikin haƙƙoƙan Manzon Allah (SAW) akanmu.

Daga abin da ya gabata, mu na iya cewa, matsayin 'yan Shi'ah a game da **Ahlulbaiti** matsayi ne na, a laɓe ga sabara a harbi barewa. Babu gaskiya a cikin riyawar

[85] Raudhah, Shafi na 107.

da su keyi na sonsu da kuma kariyar haƙƙinsu. Kamar yadda babu gaskiya a cikin riyawarsu na cewa, akwai takin saƙa tsakaninsu da sauran almajiran Manzon Allah (SAW).

A yayin da 'yan Shi'ah su ka riƙi matsayin da muka gani na raba gidan Manzon Allah (SAW) kashi biyu, su ka tuhumci mafifitan wannan al'umma da cin zalun, da keta alfarmar Manzon Allah (SAW) a game da iyalansa, su dai Ahlus Sunnah sun bi tafarki na tsakiya, wanda ya ƙunshi sanin girman gidan Manzon Allah (SAW) da ba mutanen gidan haƙƙinsu, ba tare da wata wariya ba a tsakaninsu ko haifar da husuma a tsakaninsu da sauran musulmi.

Za mu sake jaddada tambayarmu ga mai karatu, kuma muna ganin amsar tambayar a yanzu halarce ta ke a tunaninsa:

**Su wane ne masoyan Ahlulbaiti?**

Wassalam.